[8/5, 9:44 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💦💧ZATO NE💧💦
NA

HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY

MAMAN ISLAM

Daga marubuciyar

ABINDA YAKE,RAINA
WAYYO RAYUWATA

Da sunan Allah mai rahama dajin kai Allah kayi dadin tsira ga shugaba ja gaba annabin rahama annabi Muhammad S A W tareda dukkan a halinsa da sahabbansa da wanda sukabi bayansa har izuwa ranar karshe

Sharhi wannan labarin kirkirarren labarine banyishi dan cin zarafin wani ko wataba duk wanda yaga labarin yayi daidai da rayuwar shi arashi ne

GARGADI

Ban yarda wani ko wata ya juyamin labari ta kowane irin sigaba yin hakan batare da izininaba babban kuskure ne dan haka a kiyaye

PAGE 1

................wani katafaren gidane k'aton gaske mai dauke da k'aton get ruwan toka, a hankali na tura get d'in gidan wanda da k'yar na iya bud'eshi.

Wani mahaukacin farfajiya ne mai girman gaske a kalla in za ajera motoci zai d'auki fiye da ashirin.

Duk da kasan cewar gabana yafad'i da ganin girman gidan, hakan bai hanani bin gidan da kalloba, filine kamar jeji

Sannan duk da girman gidan haka bai hana an baibayeahi da wasu fararen dutsuna masu k'yalliba ga fitulu nan kewaye haskene fetal kamar rana.

Kaina tsaye na nufi ainihin k'ofar da zata sadani da cikin gidan, Allah ya temakeni nasami k'ofar glass d'in abud'e da sauri na lallab'a na shige kamar b'arauniya,

Wata kyakykyawar farar mace na hango wacce akalla zatakai shekaru sittin da bakwai zuwa da takwas.

Wani farin saurayi na gani wanda bana ganin fuskarsa domin agaban matar yake azaune ya sunkuyar da kansa k'asa da alama maganar mai muhimmanci ne.

Da sand'a nabi ta gefansu na wuce inuwata yasa matar d'agowa nayi maza na b'uya abayan d'ima d'iman kujerun da sukayiwafalon k'awanya.

Sosai na soma k'arewa katafaren falon kallo wanda bashi da wani tarkace inbanda rukunin kujeru wanda ak'alla ya lamushe set hud'u kuma ko wane rukuni akwai wani k'ayataccen centre table na glass atsakiyansu.

Sai da na ma matsa kusa da matar sannan naji abinda take cewa," ABDUL MAJID gaskiya ban

yarda ka k'ara d'auko wani auren yanzuba har sai komai ya lafa kana ganin fa irin abinda yake faruwa, bai zan hanaka aure bane amma ina soka da kata tukun har zuwa komai ya lafa kafin musan abinyi"

Wanda aka kira da Abdul majid ne naga yad'ago kansa, saida na firgita da ganin kyawunsa da cikar kamalarsa kyakyawane ajin farko fari tas kamar balarabe, manyan idanunsa ya zubawa matar wanda suka rune sukayi jajur kafin yace

"Amma nifa bani na tsuro da maganar aurennan ba Daddy ne kuma nayi nayi abar maganar amma yak'i ni kaina banason zargin da mutane suka soma min akan matsalar da bansan daga ina takeba, had'e hannayensa yayi waje d'aya alamun rok'o yace Amma kisa Daddy ya janye wannan maganar dan Allah"

Ya k'arasa maganar cikin wata irin murya mai ban tausayi,
Ajiyan zuciya Amma tayi kafin tace "shikenan Abdul zan kira shi alhajin gaskiya ya kamata a duba lamarin dole akwai abinda yake faruwa tashi kaje Allah yayi maka albarka"

"Amen" ya amsa sannan ya mik'e a hankali cikin takunsa na nutsuwa amma tabishi da kallon tausayi ya fice ya nufi bangarensa

Yana shiga d'akin ya fad'a saman k'aton gadonsa yayi rigingine yana kallon rufin d'akin fara tuno abinda yake faruwa dashi

Asalin labarin

Malam Amadu wanda yaran 'yan uwa sukafi kiransa da Baffa. Madu haifaffen garin gombe ne a yankin bajoga, yakasance kyakyawan balutani, mai cikar kamala da haiba mutum ne mai mutuk'a kirki da dattako, shi kadaine mahaifinsa ya haifa baffa yusifa wanda bayan haihuwarsa babu dad'ewa ya rasu sakamakon harbin maciji wanda ya harbeshi agona take ya rasu ko shurawa baiyiba.

Bayan rasuwar baffa umar babu jimawa itama Inna Hassu mahaifiyarsa ta rasu sakamakon annobar amaida gudawa.

Sai rik'onsa yadawo hannun innarsa Inna laraba wanda itane taci gaba da rik'on Amadu sosai take kula dashi tabashi tarbiyya daidai iyawarta.

Shekarar Baffa Amadu ashirin da d'aya kacal Inna laraba ta had'a aurensa da d'iyarta mai suna Rabi'a .

Shekara daya da auren Allah ya albarkace su da yaro namiji wanda akasawa sunan malam yusif mahaifin Baffa Amadu

Shekaran yusif biyu aka haifi ramatu, daga ramatu sai Rudwanu, sai Hafsat wadda taci sunan mahaifiyar Baffa Amadu.

A kuma tak'inne Allah yayiwa inna laraba rasuwa wanda mutuwar bak'aramin girgizasu tayiba somin Inna laraba makarace d'auki duka.

Bayan rasuwar Inna laraba yara biyu Rabi'a ta k'ara haifa Abubakar da umar daga kansu haihuwar ya tsaya mata sosai Baffa Amadu wanda yaranshi suma suke kiranshi da haka yabawa yaransa ilimin addini dana boko, boko kuwa mai zurfi daga mazan har matan duk da kasancewarsa ak'auye bashida duhun kai ko kad'an.

Kowanne mazan babu wanda baiyi degree da masters ba yayin da matan sukayi N C E yanzu haka duk sun manyanta dan babu yaro ko daya a gaban Baffa kamar yanda yaransa da jikokinsa ke kiransa.

Duk ya aurar dasu har suma sun hayayyafa .

Abdul maji d'ane ga Alhaji yusif shahararren d'ankasuwar daya tara dukiyar da baisan adadinshiba yana da gidajen mai dayaea acikin gombe da hanyoyin k'auyenta.

Yaransa biyu kacal a duniya Abdul majid da Rabi a wadda suke kira meema sosai ka sangarta meema kasancewarta mace kuma 'yar auta sun bawa yaransu ilimin adduni dana zamani wanda yanzun haka Abdul majid yake babban likita, wanda mahaifinsa da kansa bai yarda da aikin gomnati ba dan haka ya bude masa asbiti tasa takansa kuma hakan bai hana Abdul majid temako ba domin da talaka da mai kud'i duk nasane.

Bayan k'are karatun Abdul majid da murnan bikin bud'e asbitinsa, sai ya bijirowa da mahaifinsa maganar aurensa da Rashida yarinyar da suka had'u acan Gemany.

Dama abinda alhaji yusif yake bid'a kenan dan haka bayan dogon binciken da akayi akan tarbiyyar yarinyar manya suka shiga maganar aka tsaida lokacin aure

Ana saura sati biyu biki Rashida sun fita kasuwa siyayya da mamanta aka nemeta sama ko k'asa aka rasa babu irin neman,da aba'ayiba amma babu ita babu alamunta.

Bakaramin rud'ewa Abdul majid yayiba domin yana mutuk'ar son Rashidat yarinyace nutsatsiya wanda kud'in iyayenta baisa ta lalata tarbiyantaba haka kuma fita karatu acikin turawa baisa ta watsar da addinintaba.

Saida suka kai repot har wajen 'yan sanda aka baza hotunata wa gidajen t v da 'yan jaridu amma babu wani labari k'arshe iyayen Rashidat ne suka dawo bawa Abdul maji hak'uri domin ba k'aramin mummunan hali ya shigaba.

Bayan komai ya lafane an d'ebi shekaru biyu dak'yar daddynsa da mammy suka sha kansa ya kuma neman. Wata yarinya Nafisa.

Sosai suka shak'u da Nafisa domin ita irin mutanannan ne masu barkwanci da abin dariya bak'aramin d'ebe masa kewan Rashidat tayiba ita kuma ana ya saura kwana Uku d'aurin auren tashiga band'aki wanka umminta tajiyo firgitaccen ihun datayi koda ta shiga sai gawar ta ta tarar anyi mata yankan rago.

Wannan al'amari saida yai sanadin kwanciyar Abdul majid agadon asbiti wanda yajima sosai baidawo hankalinsaba

Wasa wasa saida Abdul majid ya nemi aure sau hud'u biyu dai suma b'acewar sukayi ba angasuba sama ko k'asa annemesu anrasa.

Hakama Daddyansa sau biyu yana nemar masa y'a'yan kannensa d'iyar mama Hafsa agabanta takama aman jini daganan ta hau shure shure kafin akaita asbiti ma ta cika, itako d'iyar inna ramatu itama sace ta akayi kamar shauran

Nan fa k'ananan maganganu suka soma tashi wasu suce Abdul majid d'an mafiyane wasi suce matsafine kud'i yakeyi da yaran mutane maganganuda babu dad'in ji.

To ta k'arshennnan d'iyar baba Ridwanu ce k'anin mahaifinsa itama dai gawar tata aka samu a d'akinta da kwalaben guba wanda dangi suke zargin ta kashe kanta ne domin dama ta nuna bata son auren.

Wata biyar kacal da rasuwan Amina Daddynsa ya kuma b'ullo masa da wata fitinar ta d'iyar abokinsa.

Wata irin ajiyar zuciya Abdul majid ua sauke lokacin da ring d'in wayarsa ya katse masa dogon tunanin da yatafi.

Saida gabansa ya fad'i lokacin da yaga daddynsa ne yake kiran.

Da sallama ya ya soma kafin yace "barka da hutawa Daddy ya offoce?"

Batare da yabashi amsar tambayanshiba yace "kana ina?"

"Ina d'akina"
"To kazo ina son ganinka"
Amsawa yayi sannan ya mik'e asanyaye ya tafi amsa kiran mahifinnasa

Shin meyake faruwa da Abdul majid? da gaskene shid'in d'an mafiyane ?ko shan jini ko kuma shid'in matsafine?

Muje zuwa zamuji komai a hankali

Taku har kullum maman Islam
[8/6, 1:51 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💦💧ZATO NE💧💦
NA
2020
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY

MAMAN ISLAM

DAGA MARUBUCIYAR

ABINDA YAKE RAINA

WAYYO RAYUWATA

Naji dadin yadda naga labarin yasami karbuwa fiyema da tunani ina kaunar ku masoyana aduk inda kuke nima ina tare daku

Page 2

............da d'an saurin sa ya shige toilet, ruwa ya watso ya fito cikin sauri ya shirya cikin wando tree quater da 'yar singlet mai fad'in hannu farare k'al

Afalon sa na musamman ya sameshi tareda Mammynsa, yak'arasa a nutse da zube agabansu yana gaidasu.

Cikin nazarinsa Daddy yake kallonsa kafin ya turo masa abincin dake gabansa yace "d'auka kaci Abdul magana nakeso muyi dakai"

Duk dayake baya cikin yanayi mai dad'i hakan baisa yayiwa mahaifinsa musu ba dan babu wannan atsakaninsu.

Tusa abincin kawai yake kamar anmasa dole yayin da Mammy ta k'ureshi da ido tanajin kamar tafashe masa da kuka, wani irin tausayin d''annata ne yake dawainiya da ita.

"Abdul" Daddy yakirashi yad'ago a hankali ya sauke manyan idanunsa akan Daddyn kafin ya amsa a hankali "na'am"

"Kasan abinda yasa nace ka auri Yusra 'yar ahaji Lawan?"

Kai ya girgiza masa batareda yace komaiba

Saboda abinda yake faruwa kaga har mutane sun fara camfaka kuma gaskiya bana so maganar mutane yaci gabada tasiri akanka shiyasa nakeso mubawa yarinyar temako da kariyan da idanma wani abune yake bibiyanka zai bayyana bada jimawaba insha Allah"

Har lokacin kansa na k'asa bai iya musu da mahaifinsa ba kuma zai fara daga yauba dan haka yace

"Shikenan Daddu Allah yakawo k'arshen abin kamar yadda kuka ce"

"Shikenan tashi kaje kafara shiri daga yau zamuyi komai ab'oyene hatta 'yan uwana bazasu san da wannan batunba domin ina da ayar tambaya akan duk wani makusancina Allah yayi maka albarka"

"Amen" ya amsa acan k'asan mak'oshi ya mik'e kamar wani mara laka yafice yayin da mahaifiyashi ta bishi da kallo har idanunta ya ciko da hawaye.

Dafata Daddy yayi yace "Amina ke uwace kici gabada yiwa d'anki addu'a komai zai wuce da yardar Allah".

Kuka tafashe dashi tafad'a jikinsa tace" alhaji ianajin tsoro nakeji alhaji kullum addu'ar mukeyi munasawa ayi mana amma kullum abin sai gaba yakeyi ina,tsoron,kar yarona yazauce plss alhaji idan aurenne,matsalar abarshi haka mana".

"A a Amina karkice haka ina wannan juriyan da jajurcewannaki dan Allah karki karyar damu domin kece kwarin gwaiwarmu"

.tace "shikenan Alhaji Allah yakawo k'arshen abin"
"amen ya amsa.

"Yauwa alhaji naga an bud'e wancan fat d'in anagyarawafa?"

Dubanta yayi yaga yadda ta tsareshi da ido tanajiran amsa murmushi yayi sannan yace " amarya zan kawo miki wacce zata temaka miki da 'yan aiyukan gida"

Yafad'a yana gimtse dariyar dayataso masa ganin irin kallon data k'ureshi dashi kafin tace

"Kishiya fa alhaji naji kana kirq da girmana,da komai ai wannan ma abin kunya ne, to wallahi abinda bazai sab'uba kenan bindiga a ruwa karma ka soma ta fad'a cikin fad'a fad'a.

Dariyan dayake ta dannewa ne yakwace masa kafin ya d'an shafi gefen fuskanta yace "o ni Ishu kishi harda su tsofi?"

Hararan wasa tayi masa kafin tace "alhaji kenan inbanyi kishinka ba to kishin wa kakeso nayi? Kainefa gatana komaina rayuwata kai karabani da maraicin danake ciki mai da danginka dangina kabani kulawar da nagaza samu awajan gwaggonnina ka gayamin taya bazanyi kishin kaba?"

Ganin har idanunta sun canja kala alamun tana son tayi kuka ya rungumeta yace

"Ya isa haka nima wasa nake miki Abunakar ne zai baro can misra zai dawo nan da zama tareda iyalansa gaba d'aya, saida na bari yagama duk wani shiri nasa sannan na fara aikin wahen bakiga angamaba fenti akeyi?"

Wani irin farin ciki ne yakawowa zuciyar hajiya Amina farmak'i dajin dawowar su Abubakar dan duk matan k'annen mijin nata nasu yafi zuwa d'aya da Ummu kursum tana da mutuk'ar kirki ga

ilimi da sanin yakamata ita 'yar k'asar misran ce inda acan ta had'u da Abubakar wanda karatune yakaishi can bayan ya kammala sukabrik'e shi yayi musu aiki saboda mutum ne wanda yatara ilimi mai yawan gaske.

Yaransu uku biyu maza daya mace FATIMA itace babbar 'yarsu wacce takasan kyakyawar gaske sak mahaifiyarta babu ta inda ta baro mahaifiyarta wajen kyau da diri ga nutsuwa tuni tajima da saukar karatun ta tana hadda yanzun,haka tana,da hadfan izu talatin da d'aya akanat, sannan a wannan shekaran tagama karatunta na secindry wanda amsar takardunne ma yasa su jinkirta dawowa nanja.

Sai k'annen ta wanda 'yan biyu ne Abdul samad da Abdul Rashid yarana masu kyau kamar 'ya'yan larabawa fulanin asali kenan su kuma mahaifinsu suka d'auko

Sosai Fatima taji dad'in dawowarsu Nigeria domin jininsu yayi masifar had'uwa daba Meema k'anwar Abdul majid suna shiri sosai.

Tunda Abdul majid ya koma d'akinsa sai kawai naga yakasa zaune,ya kasa tsaye, sai faman zarya yakeyi yayin da zuciyarsa yake wani irin bugu mai k'arfin gaske idanunsa suka kad'a sukayi wani irin ja mai abin tsoro, kuka yake sonyi amma zuciyarsa tak'i bashi had'in kai.

Tashin hankalinsa, damuwarsa, fargabarsa rayuka bakwaine suka sulwanta ta dalilinsa amma duk Daddy bai duba hakaba yake neman kuma jefashi cikin wani halin nada ban.

Komanshi yanzun yayi baya Abdul majid mutum mai faran faran da jama'a gashi dasan na k'asa dashi sam baya d'aukan kansa shi wani yana mu'a malantar mutane dai dai yanayinsu.

Dak'yar yasamu bacci ya d'aukeshi wanda bai farkaba sai ana kiran assalatu saboda bai samu bacci da wuriba yasa d'an tashin daren dayake yi ma yau bai sami damar yiba.

Kasancewar yau d'in ranar juma ace kuma bai cika fita aiki ranan ba yasa baima fitoba kwata kwata sai Meema ce takai masa abin karinsa d'aki.

Lokacin yana zaune saman sofa yana ta faman danne dannen wayarsa wanda yanzun yazame masa abokin hira.

Da sallama tashiga d'akin, batareda tajira amsarshiba ta je tajera masa kayan agabansa, har ta mik'e ya buga mata wani irin tsawa.

Jiki narawa ta koma ta tsuguna agabansa cikin kakkausar murya yace "daman anan kike ajiye abincin idan kin kawo?"

Cikin rawan jiki dana murya tace a a yaya dama dannag.......

"Dalla mamala kwashe ki maidasu derning ai da sauri ta kwashe kayan jiki na rawa ta nufi derning d'in dasu, tuni idanunta ya ciko da hawayen tausayin yayannata, duk wannan abinda yake faruwa dashi yamai dashi wani irin mafad'aci mai zafin rai.

Har ta kai bakin k'ofa yad'ago yana duban yadda k'anwar tasa take ta faman sharar hawaye, kiranta yayi, ta dawo ta durk'usa agabansa ya mik'o mata hannunsa ta rik'e nasa ta fashe da wani irin kuka, sosai take tausayin yayannata tareda jimamin halinda yake ciki.

Saida ya rarrashita ya ringa bata hak'urin fad'an da ya hauta dashi ba gaira ba dalili sannan ya sallameta.

Bayan ya d'an tsakuri abincinne kuma yayi wanka ya shirya cikin kananan kaya blun wanda da da riga ruwan toka ya gyara sumar kansa mai uban yawa taje uban k'asumbar daya tara.

Ya fito kenan yaga na shigo da kayan d'aki sabbi ana nufar b'angaren dayaga ana gyrawa, wanda duk a tunaninsa shi akewa gyarn auren da ake shirin k'ak'aba masa, dan Daddy yace agidan yakeson su zauna da Yusra.

Take yaji wani irin k'unci ya mamaye masa zuciya.

B'angaren Amma ya nufa dan gaishe ta, yana sallama abakin k'ofar yaji an rungumeshi an cikwaikwaiye shi tareda ihun murna.

Sosai ya ware idonsa akan fuskarta yana mamakin yaushe sukazo dan tashin hankalin dayake ciki yasa shi mantawa da cewa Abbu da kansa ya fad'a nasa zasu dawo nan da zama,

Kallonta yake da mamaki yace "Fatina?"
Dayake haka yake kirantactun tana yarinya ita kuma tankance yayana tun bata iya fad'aba har tazo ta iya,.
Itama da mad'aukakin fara'a ta dube shi tace "yayana"

Wani irin rungumeta yayi ajikinsa yanajin wani irin tsoro yana saukar masa wanda baisan dalilinsa ba sosai ya k'ank'ameta har sai da tasaki k'ara tace "yayana zaka b'allani fa"

Sannan ya sassauta mata rik'on hannunta kama suka shiga falon Amma, nan yaga abin mamaki Abbu da Ummi zaune gaban Amma sunata hira har da mammy da Umma matar kawu Ridwanu da anty Ruk'aiyya matar Abba Usman yasha mamakin ganinsu.

Yasan sarai kan iyayensu a had'e yake basuda yawan fad'a ko gulmace gulmace irin na faccaloli sam bazaka tabajin kansuba.

A hankali ya k'arasa kusa da Amma yasami waje ya zauna yayin da Fatima ta zaune kusa dashi har kafad'ansu yana gugar juna.

Gaida su yayi suka amsa da kulawa Ummi ta dubi Mammy tace "yarona yayi ciwone naga ya rame dayawa haka?"

Ajiyan zuciya Mammy ta sauke tace

Taku maman islam
[8/7, 8:29 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💦💧ZATO NE💧💦
NA

HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY

MAMAN ISLAM

DAGA MARUBUCIYAR

ABINDA YAKE RAINA

WAYYO RAYUWATA

Page 3

...............bari kedai Ummu wallahi abinne bansan ta inda zan bulloba,
Kallon juna,Umma,da anty Rukaiyya sukayi batare da sun lura da kallon da Abdul majid ya binsu da shiba wata alama,sukayiwa juna wadda sukad'ai suka san ma'anar hakan.

Mik'ewa yayi tareda cewa "bari naje d'aki akwai abinda nake son k'arasawa" Amma tace "anjima kadawo nadama maka furar tanan afirij"
Yace "bani kawai natafi da ita nasaka afrige d'in falona"

Fatima da tamik'e tana shirin binsa Amma ta duba tace "d'auko masa furar nan da Meema tasaka afrige d'azu.

Da sauri ta d'auko masa tayi waje batare da ta mik'a masa mug d'in ba, yabita da kallo yana murmushi kafin yace ma iyayennasa sai anjima

A can bakin pat d'insa ya sameta atsaye, ya lakace mata hanci yace "gundura tadawo" kallonshi tayi tace yaya meye gundura kuma?"

Domin hausa bai ishi bakinta ba, baice mata komai ba yaja hannunta suka shige falon tasaka furar afrige tadawo ta zauna akusa dashi tace "yayana labarifa zaka bani"

Kallonta ya rinkayi kafin yace "wanne irin labari zan baki.

Abangaren su mammy kuwa bayan sun koma b'angaren mammy dan har lokacin ba'a gama gyara mata pat d'in taba.

Anan ta kwashe duk abinda yake faruwa da Abdul majid tafad'awa Ummu Kulsum, sosai ta girgiza dajin wannan mugun labarin, ta dubi Mammy tace.

"Anya mammy ba alajanune suka tab'a yaronnan ba ?"

Mammy tayi wani murmushi mai ciwo tace "babu wasu aljanu domin gurin rukiyya babu inda bamujeba amma ko gezau "

Ummi tace to gaskiya akwai ayar tambaya dan haka zama bai ganmuba domin idan akace mun hak'ura anci gabada tafiya a haka akwai babbar matsala fa.

Mammy tace "bana iya bacci Ummu kullum cikin kuka nake da addu'ar sauk'i wa yaronnan wallahi karkiga yadda nake tausaya nasa Abdul yana da matuk'ar hakuri, zai wuya ya fad'a miki damuwar sa".

Ummi tace "karki damu mammy nima Abdul d'anane nayi miki alk'awarin sanar da baffi" dake mahaifinta babban malamin addini ne anan misra.

Mammy tace "shikenan Allah yasa adace"

Ummi tace" tace insha Allahu za'a dace "

Ido ta tsareshi dashi tare da zuba tagumi da duka hannayenta, hura mata iska yayi a idanun, ta lumshe idon ta kuma bud'esu akansa.

Hannunta ya rik'o shima ya zuba,mata nasa idanun sosai ya had'e idonsa danata take ta had'e rai gami da kawar da kanta tace "nifa bana sonkallo"tafad'a da sigan shagwab'a.

Shima kwaikwayan muryanta yayi "to nima kidaina kallona"

Had'e rai tayi ta tashi zata fita, ya fusgota tafad'a jikinsa yarik'eta ajikinsa yace

"Ina zakije kuma muna hira k'ok'arin tashi take a jikinsa yak'i bata damar hakan ta hanyar k'amk'ameta ajikinsa yace "wai meye hakane ki zauna wata magana zan fad'a miki mai dad'i

Jin haka yasa tagyara zamanta tace "yauwa nawan dama inaso muje bajoga kaga sau d'aya na tab'a zuwa"

Yace "to zamuje amma ba yanzuba sai kin huta kinga yau kuka zo"

Tace "yauwa yayana naji ana tasa lokacin bikinka awajen Ummi meyasa kuma nazo nasamu babu mata?"

Take yanayinsa ya sauya d'an farin cikin dayasa mu daga gareta yab'ace ba't kalan idonsa ya sauya yayi jajir

Kuyi hakuri wllh nagaji unguwa naje yau.

Taku maman islam
[8/8, 5:12 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💦💧ZATO NE💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM

DAGA MARUBUCIYAR

ABINDA YAKE RAINA

WAYYO RAYUWATA

Page 4

....................ya kalleta da wani irin yanayi mai wuuar fassara, batareda yace mata komaiba.

Ita kanta saida ta tsorata daganin yanayinsa, take idanunta suka ciko da kwalla, ya dubeta cikin tashin hankali domin hawayen Fatima fitina ne ga zuciyarsa.

Tallafo fuskanta yayi da duka hannayensa yaja daf dashi har numfashinsu na bugun juna, take yanayinsu ya sauya wani irin kasala ya rufesu dukansu basu saba da irin yanayinba.

Cikin sanyi murya wacce take d'auke da tsantsar tashin hankali yace "Fatima karkiyi kuka zan

fad'a miki dukkan abinda yake faruwa, duk danasan cewa har yanzu bakiyi hankalin da zaki san me hakan yake nufiba"

Take ya kwashe dukkan abinda yake faruwa ya fad'a mata wanda kafin yagama har shid'ewa take sabo da kukan datake gurza.

Wani irin tausayin yayan natane ya rufeta ta d'ora hannayenta saman fuskarta hawayenta yana cigaba da kwaranya.

Janyota yayi sosai tashiga jikinsa yana dubanta da idaninsa da sukayi wani irin ja, shima kad'an ya rage yayi kukan yace

"Fatima plss ya isa haka dan Allah ki daina zan iya mutuwa fa kinji yadda nakeji kuwa saboda wannan kukan da kikeyi?"

Yafad'a tareda kamo hannunta ya d'ora asaitin zuciyarsa.

A firgice ta d'ago rinannun idanunta tana kallonsa, saboda wani irin bugu da zuciyarsa yakeyi abin har ya zarce k'a'ida, take wasu sabbin hawayamen suka kuma zubo mata.

Hannu tasa itama ta tallafo fuskarshi tana dubansa tace "yayana tabbas kana cikin wani hali amma kasani ni banyi k'ank'atar da zan kasa gabe halin dakake cikiba yayana, karka manta kaine d'an uwana wanda nafi shak'uwa dashi kaine mafi soyu acikin 'yan uwana ko Ammar da Yaseer banajinsu araina kamar yadda nakejinka yaya".

Shiru tayi tareda share hawayen da yak'i tsayaea tun d'azun kafin tacigaba da cewa "yayana ina tareda kai, duk wani matsalarka nima nawane, dan haka kasa aranka zamu yi maganin wannan abun da yardan ubangiji, ka daina sawa ranka wannan abun yafi k'arfinka tunda babu abinda yafi k'arfin ubangiji dan haka mubar masa komai"

Cikin sanyi jiki ya mannawa hannunta da ke cikin nasa wani sassanyan kiss yace "nagode

k'anwatacAllah yayi miki albarka Allah yasa ki gama lafi".

Ranan anan ta wuni wajensa harda Meema da ta nemeta bata samuba tasan tana wajensa sosai meema tayi mamakin ganin ya d'an saki jiki suna shan hira da Fatima har itama yana sata aciki.

Kodayake ba abin mamaki bane idan akayi duba da irin shak'uwar dayake tsakaninsu, ita kanta Meeman saida tabata hak'uri abisa yanda ya rik'ayi mata komai da zafi zafi.

Dake daman Abdul majid mutum ne wanda yake mutuk'a jan nasa ajikinsa.

Talatainin darene misalin k'arfe biyu da kwata naga wani mutum ya tashi daga shimfid'arsa, saida ya lek'a fuskar matarsa yaga tana bacci hankalinta kwance babu abinda yake damunta.

Cikin d'auke numfashi da sand'a na ya lallab'a yafice daga d'akin a hankali ya maida k'ogar ya rufe dan kar motsin rufewar ya tasheta.

Cikin gidan nasa naga ya nufi wani lungu mai duhuwa wanda shuke shuken fulawowin wajen ya k'arawa wajen duhu.

Bayan yayi tafiya mai yawa sosai har yagaji lik'is sannan naga nufi wani k'atoton get mai girman gaske wanda bud'e shima sai k'arti majiya k'arfi.

Wasu maganganu naji yafara wanda ban fahimci abinda yake cewaba,kafin na ankare kawai naga get d'in ya bud'e kansa, yana shiga nabi bayansa da gudu sauara k'iris k'ofar ya datse min k'afa dan yana shiga naga yafara rufe kanshi, shine dalilin dayasa nabisa da gudu.

Wani irin haske nagani tarwai tare da wasu irin kitika kitikan masu wani irin murd'ad'd'an jiki

naga suna ta zarya abakin k'ofar kamar mayuntan zakuna daganinsu k'iris suke jira su dumawa mutum wawa

Sosai yanayin mutanen zai gurgitaka domin babu alamun rahama a idanunsu bak'i k'irin suke yayin da idanunsu ya kasance jajur kamar garwashin wuta.

Take jikina yafara rawa amma dan masifa ban fasa bin bayan mutumin danaga wannan mutanen suna zubewa suna masa sujjada ba innalillahi wainnailaihi raji un.

Wai mutum abokin halitta d'an uwansu sukewa sujjada kai Allah kafisshemu tab'ewa.

Tunbayana tafiya cikin mutane naga yadawo bin hanyar da babu kowai sai uban duhu da lalube na rik'a bin bayarsa har muka isa wata 'yar siririyar hanya wacce ta mik'e d'od'ar har wata 'yar k'aramar k'ofa kamar gida mukulli naga yasaka ya bud'e k'ofar ya shiga sannan ya maida k'ofar ya rufe.

Tundaga tsakar gida na fara ganin gawawwakin mutane abinda ya mutuk'ar firgitani nasaki wani k'ara ba shiri na toshe bakina nayi wani d'an lungu garin b'uya natake wani abu mai taushin gaske dake tsabar fitina dazan biyoshi cire takalmana nayi dan kar yaji takun tafiyana yasan ina binsa, idona na d'ora akan abinda na take me zangani innalillahi wainna ilahiraji un gawar jaririne wanda da alama ba adad'e da kasheahiba

Kuka na fasheda shi shikenan na kawo kaina inda tawa zai k'are nima.

Tafiya naga mutuimin yaci gaba dayi ya kuma bud'e wata k'ofa mai murfi biyu saiga wani k'atoton gunki mai siffar mace tsirara yana aman jini yayin da jinin ya malala ki'ina na d'akin

Muje zuwa karku bari abaku labari

Maman islam
[8/9, 3:56 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💦💧ZATO NE💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM

DAGA MARUBUCIYAR
ABINDA YAKE RAINA
WAYYO RAYUWATA

Page 5

..................sai yanzu naji mutumin yayi magana da kakkausan murya naji yana cewa, "meyasa za'amun haka meyasa bafa haka mukayida keba kinyimin alk'awarin duk abinda na nema zan samu me yasa wannan yake neman gagarana me yasa meyasa????"

Shine abin da naji mutumin yacigaba da maimaitawa, ga mamakina kawai naga wannan gunkiyar ta bud'e ido al'amarin dayasa naji cikina yayi wani irin murd'a kafin na dawo nutsuwata kuma saijin muryan nayi kamar da aradu take wani masifaffen futsari ya kubce min sakamakon jin wannan mugun muryan.

Wani irin murd'awa cikina yaci gabada yi saboda ganin yadda idanun gunkiyar yake balbala da wuta ci take sosai har tana laso goshin gunkiyar, babu shakka gani da jin wannan mugun abun saida nasaki gudawa mai k'ara wando wanda badan hargagin wannan mugun halittanan ba babu abinda zai hana mutumin nan jin k'aran jerin gwanon tusan danake ta b'urkawa saboda gudawar mai k'arane.

Jinai abin yacigaba da cewa bamu bane bama bibiyan bayanka saboda kanayi mana duk abinda muka sakaka, kuma muma labari ya ishenu dan haka kaci gaba da bincike mu tuni namu yayi nisa karka damu bazamu bari acutar mana dakaiba.

Wani irin ajiyar zuciya mutumin yasaki sannan naji yace "nidai banaso asirina ya tonu, nafison koda asirin zai toni to abari nayi k'arfin da babu wata hukuma da ta isa tajadani".

Jinai mugun halittan yace 'mai lalata maka shiri mafi kusa dakaine idan lokacin kasan kowane yayi zaka sani"

"Ataimaka abad'amin kozansan hukuncin dazan d'auka akansa domin al'amarin yafara bani tsoro"

Gunkin yace"kai idan yafi k'arfinka mu kasan baifi k'arfin tsafinmuba, dan duk duniya gunki d'ayane yafi k'arfin tsafinmu, kuma da sannu zamu had'aka dashi da zarar kagama mana aikinmu"

Yana gama fad'an haka kirib idanun suka koma yadda suke jinin yaci gabada kwarara, da sauri naja baya ganin mutumin zai fito.

"Yaya dan Allah kayi sauri kasan gwaggo Hafsatu bata son jinkiri tunjiyafa na bata labarin munanan tafe ni wallahi na k'agu naga gari tunda mukazofa babu inda nafita ina sank'ame agida"

Tunda tafara maganan yake bin libs d'inta da kallo yanda take maganar kamar wanda take tsara abin da salon yanga.

Ido ta hure masa yayi firgigit yana kallonta da ido tayimasa alaman kallonfa?
Sosa k'euansa yayi tareda d'auke kansa batare dayace mata komaiba.

Ganin haka ta kama tsallen shagwab'a tana fad'in "ni wallahi yaya kadena min irin haka sai magana nake kayi min shiru, saiga hawayen shagwab'a shar shar .

Take ya rud'e ya rik'o hannunta yana fad'in "haba babyna meye haka dan Allah?"

Tace "bakaine ba kak'i kashirya mutafi kasanfa da tafiya daganan zuwa bajoga gashi kuma tuni azhar ya wuce"

Hannu yasa yana goge mata hawayen tareda fad'in "to ya isa kark8sakani kukan nima maza jeki k'ara wanke fuskarki ki shafa hoda da jambaki kafin na gama shiyarwa"

Yana gama fad'in haka ya shige toilet yayin da ita kuma ta juya ta fice d'akin kai tsaye bangaren mammy ta nufa.

Meema ce zaune falon tana ta faman danne dannen wayarta, wani kallo Fatima tayi mata kafin tace"haba dear wannan wanne irin wulak'ancine kina sane zamu fita amma dubeki dan Allah a zaune ko shiri bakiyiba?"

Harara Meema ta galla mata kafin tace "wallahi yariyanyar nan baki da kunya ina katsayin yayarki kikemin fad'a sai kace wata sa'arki?"

Dariya Fatima ta shek'e dashi kafin tace "su yaya manya dukafa wata uku ne tsiranna mu, ai idan wani yajima sai ya d'auka irin shekara biyunnan kika bani ko uku ni dallah malama jeki shirya, gayaya can ma yana shitinsa.

Meema tace "nifa babu inda zani bakiga yadda garin yake shan kunuba sanin kankine idan nafita akayi ruwannan akwai matsala"

Juyawa Fatima tayi ta shige d'akinsu nanan b'angaren tabbas tasan cewa idan Meema ta shiga ruwa sai ciwonta na limoniya ya motsa dan haka batayi mata gardamaba ta wuce ta hau shirinta

Wani dandatsetden less taka mai mutuk'ar kyau da tsada kalar sky blue ba k'aramin kyau tayiba ta kafa d'aurin d'ankwali mai kyau da tsari kamar irin k'atuwar 'yar tsanan nan haka takoma kamanninta da mamatan na balarabiyan asali,ya fito.

Tana fitowa falon dai dai shima ya fito kafeta yayi da idanu babu ko k'ibtatawa yayin da zuciyarsa take wani irin bugu kamar zata fasa k'irjinsa.

Ita kan meema ido ta kafe ta dashi na kallon,tsabar tsagwaron kyau gaskiya Fatima badai kyauba Allah ya d'iga baiwarsa anan wajen.

Ganin irin kallon da yaya da k'anwar suke binta dashi yasa ta hau dudduba jikinta ko wani abin kallonne ajikinta.

Ganin baya ga komai bane yasata tamabayar Abdul majid da ido ko akwai abinda yagani ajikinta?
Hararan wasa yayi mata sannan yace "gani nayi ko kyau bakiyiba ko k'anwata?"

Ya k'are magananshi da tambayar meema wadda take ta danne dariyanta ganin yadda Fatima ta had'e rai

Dole tasaki dariyan datake b'oyewa ganin har idanunta yafara cikowa.

A hankali ya k'arasa kusa da ita ya dafa kafad'unta ya d'anjata jikinsa cikin rad'a yace "muddun kika bari hawayenki ya zubo to babu ke za'ayi tafiyannan.

Kallon Meema,yayi, yayi mata alaman tambaya da ido?

Itama batayi magana ba ta nuna masa sararin samaniya da hannun ta take ya gane me take nufi dan haka bai k'ara maganaba yaja hannun Fatima suka fice suka nufi d'akin mammy.

Sallama sukayi mata, ta d'an dubeau tace yanzu bazaku bari kuga yadda garin zayi ba awannan uban hadarin zaku fita?"

Da sauri Fatima tak'arasa gabanta tace "dan Allah dan Allah mammy wallahi tafiya a'irin wannan weather yafi dad'i"

Mammy tace "to sikenan Allah yadawo daku lafiya, hakama ummi tace musu anan dai Abdul ne yayi magana ganin Fatima ta damu da tafiyar.

Ganin yadda garin yake dad'a murtukewa yasa Fatima shiga d'akinta tad'ebo kaya kala biyu tasaka awata 'yar madaidaiciyar jaka.

Dazasu fitama dagewa tayi itace zata jasu, dole Abdul majid ya zauna faront seet ita kuma ta zauna a mazaunin draiver tayi mata key ta figa da gudu suka fice agidan.

Kasancewar batasan gariba shi ya rik'a nuna mata hanyar yayin da ita kuma take falfala gudu abinta kasancewar basubi ta babban titiba yasa bata sami matsalan cunkosoba.

Suna tafe suna hira idan yaga zata kauce hanya yayi saurin seta mata jar suka bar cikin gari suka fara shiga daji daganin yanda take tuk'in cikin k'warewa kasan cewa ta hana dad'e da iya tuk'inta.

Wani irin hadarine ya dad'a tasowa bak'i k'rin ga wata iska irin maijar k'asar nana take sukayi saurin zuge glasan motar Fatima ta gangara gefen hanya dan yadda garin yayi duhu babu damar tafiya dole su tsaya garin ya washe dan ita ba damuwarta bane tafi acikin ruwa.

Jingina tayi ajikin kujeran tana maida numfashi k'ura mata ido yayi yana kallonta, sosai yakejin Fatima ajininsa.

Ruwane ya tsuge da gudun gaske ta rik'a kallon yadda ruwan yake gudu ta gilas yayinda shi kuma ya gyara zamansa yana kallonta tareda d'ora duka hannayensa akan fuskarsa.

Juyowa tayi tanayi masa magana bayan ruwan ya lafa, amma baisan tanayiba sai da taja dogon hancinsa, sannan yayi firgi git kamar wanda yatashi abacci

D'an had'e rai tayi tace "wallahi yaya ka koyi wani irin kallon k'urillah wanda a da sam ba halinka bane"

Murmushi yayi ya d'an jata jikinsa ya mannawa goshinta kiss batare da yace komai ba ya gyara zamansa yana kallon hanya.

Jan motar tayi cikin sauri tana fad'in "bana  son muyi dare badanma ruwannan ba aida tuni mun kusa" gyara belt d'inta tayi tafigi motar, shikam kallonta yake yana mamakin yadda take gudu da motar ko tsoro bataji.

Sai da sukayi tafiya mai d'an nisa suna ta ratsa gonaki ruwan yadad'a tsugewa dan dole ta rage gudun, amma bata dakataba saboda yanzun garin a washe yake babu duhun.

Haka sukaci gabada tafiya har yanayin ya d'an sauya domin ruwan da akayi yasa garin yad'anyi duhu kad'an, awannan yanayinne Fatima taga wasu abubuwa sunfara giftawa ta gabanta da mugun gudu, shit saitaga abu ya wuce da gudu sai ta ganshi d'an mik'il.

Haka abubuwan suka cigaba da giftawa a idonta ta kalli Abdul majid da nufinyi masa magana taga shi idanunsama a rufe suke ya d'ora tafukansa asaman fuskarsa.

juyowan da zatayi domin cigaba da tuk'inta ganin Abdul majid yana bacci sukayi ido hud'u da wani k'atoton zaki mai girman gaske wanda ko alabari bata tab'a ganin irinsaba ya taho da wani irin mahaukacin gudu.

Jitai wani irin abu ya tsarga mata tundaga tsakiyar kanta har zuwa tafin k'afarta yayinda wani irin tsoro ya lullub'e ta take ta runtse idonta tana addu'a tana bud'e idon tasaki firgitaccen k'aran dayasa Abdul majid bud'e idonsa da sauri dan ganin tasaki sitiyarin motar yafara juyawa dasu.

Da wani irin zafin nama ya haye kan cinyarta batareda yasan yayi hakanba yasamu ya tsai da motar da k'yar yana maida numfashin tsoro.

Muje zuwa

Taku maman islam

[8/10, 9:28 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💦💧ZATO NE💧💦
NA

HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY

MAMAN ISLAM

DAGA MARUBUCIYAR
.ABINDA YAKE RAINA

WAYYO RAYUWATA

Page 6
......................kallon yadda ta ta kure kanta yake bayan ya koma wajen zamansa.

Wani irin rawa jikinta ya kamayi, har lokacin kuma idanunta suna kulle katamau,

Dafa kafad'arta yayi wanda yasa ta zabura dasauri ta bud'e a idon azaton ta zakinne ya k'arasa inda take, ilai kuwa tana kallon gefenta taga zakin atsaye kyam yana kallonta da wani irin jan

ido.

Wani irin gigitaccen ihu tasaka tareda furta duk addu 'ar dayazo bakinta tunda taje arayuwarta bata tab'a ganin kalar wannan zakinba me wasu irin idanu masu abin tsoro, har wuta ta hango yanaci acikin idanun nasa.

Duk jikinta babu inda baya rawa saboda ba k'aramin firgita tayiba tunda take bata tab'a ganin zaki yana tafiya da k'afa biyu kamar mutum ba sai yau.

Jawo ta Abdul majid yayi a tsorace ganin yadda take had'a uban gumi ga jikinta da har ya d'auki zafin zazzab'i tsabar firgicin da ta shiga.

Kwantar da kanta tayi akan k'irjinsa har lokacin jikinta bai bar rawaba a hankali ya kai bakinsa kunnenta yace "haba Fatima nifa banga zakin da kike ta magana akaiba duk kinbi kin rud'a kanki nima kin rud'ani ki mutsu mana kiyi addu'a babu abinda zai sameki in sha Allah".

A tsorace ta kuma bud'e idonta still yananan kuma idanunsa akanta ko k'ibtawa bayayi, wannan karon bata rufe idontaba kuma batayi ihunba.

Duk da bugawar da zuciyarta yakeyi har ya zarta k'a'ida fuskar Abdul majid ta kamo tajuyo dashi ta inda zakin yake tsaye cikin rawar murya tace "ka ganshifa kallon tuhuma yakemin me,na masa tafad'a tareda fashewa da wani irin kuka.

Kallon inda take nuna masan yayi shi kam baiga abinda take nuna masanba,yace"nifa babu abinda nagani Fatima wallahi banga komaiba"

"Bakaga komaiba?
Bakagafa komaba kace,

Ta kuma maimaitawa tareda fashewa da wani kukan taba fad'in na shiga uku na lalace" tafad'a gaba d'aya tagigice fuskarta yayi jajur saboda tsoro da kukan da takeyi.

Ganin haka yace "dawo front seet ki zauna ni najamu kinga magrib ya kawo kai"

Mak'e kafad'a tayi tace "wallahi yaya saida kayi tuk'in nan a haka babu inda zan d'ara daganan salon na koma gefe yaji dad'in zuro hannu yayi loma d'aya dani"

Kallon yanda ta k'adandane shi yayi sai kuma ya sauke nannuyan ajiyar zuciya dole sai a hakan yacigaba dajan motar tana jikinsa.

Ikon Allah ne kawai yakaisu bajoga, domin yadda motansu yake zabga uban gudu haka take ganin zakinna jere dasu dab da dab babu ta inda suka gotashi.

Saida suka sha kwanar gidan gwaggo Hafsatu tanemeshi tarasa kamar walk'iya, wata irin ajiyar zuciya tasauke tareda lumshe idonta ta bud'esu akan Abdul majid dataji ya dubgure mata kai yace "matsoraciya kawai dankinganki a gonaki shine duk kika bi kika tsure kike kiran zaki, banda abinki Fatima zakine zai ganmu yabarmu mu wuce lafiya kuma mema zai kawo zaki gona?"

Still ajiyan zuciyar ta kuma sauke sannan tace "hum yayana kenan bazaka ganeba wallahi zaki nagani da idona kuma yanzun da ace zaka kain asbiti babu abinda zai hana aga jinina yayi mugun hawa"

Dari ya kuma sannan yace "sai ki d'agani ko ai munzo gidan"

Sauka tayi ajikinsa ta fito daga motar shima ya fito suka jera suka shiga gidan.

Gwaggo Hafsatu na bakin famfo tana d'aura alwalan sallan magrib da ake ta kira a kowane masallaci dan lokacinta ya shiga tagansu.

Take farin ciki ya kamata na ganin d'iyar ka'ninta da kuma d'an yayarta tayi musu sannu da zuwa yayin da Abdul yayi alwalar ya fice masallaci ita kuma Fatima tayi tabi gwaggo Hafsatu wadda har ta tayar da tata itama ta kabbara sallah.

Abdul majid bai dawoba sai bayan sallar isha wanda har su sun idar da tasu suna gaisawa, suna ta hira da gwaggo da Fatima.

Har k'asa Abdul yagaida gwaggo ta amsa cikin sakin Fuska tana tambayarsa mutanen gidan

Yace "lafiyansu k'alau gwaggo duk suna gaida ku"

" muna amsawa "tace daga haka ta mik'e ta fice dan kawo musu abinci.

Binta Abdul yayi da kallo har kullum yana mutuk'ar tausayawa rayuwar gwaggo haihuwar ta d'aya jal aduniya kuma ta sanadinsa ta rasata.

Wasu kwalla yaji sun kawo idonsa lokacin da ya tuna halinda yake ciki tunda akayi maganar aurensa da Yusra bashi da kwanciyar hankali har kullum damuwansa shin kasheta zasuyi itama ko kuma saceta zasuyi kamar yadda suke sauya abubuwan?

Wani karon su sace wani bin kuma akashe.

Bayan sun gama cin abincinne Fatima tace "gwaggo na gaji inajin bacci zanje na kwanta"

Abdul ya dubeta yace "wuri haka rahuwa kawai"

Hararan wasa ta galla masa batareda tace komaiba ta wuce tabarshi anan suna ci gaba da hiransu da gwaggo.

K'afe d'ayan dare tafarka awani irin zabure tana addu'a addu'abud'e idon dazatayi kawai taga zakinnan gefanta atsaye ya tsareta da idanunsa da suke ci da wuta.

Wani irin razanannen ihu tasaki take fitsari ya sub'uce mata.

A tare Abdul majid da gwaggo Hafsatu suka shigo d'akin jin ihunta da sauri Abdulbya rik'eta yana tambayar "lafiya?"

Yayin da gwaggo ta hauyi mata tofi ganin irin zaburan datakeyi ita kuma kuka take tana fad'in "shikenan kasheni zaiyi yaya ya biyoni nanma.

Sam Abdul ya manta da abinda ya faru a hanya yace "wayevyabiyoki zai kasheki?"

Ya fad'a cikin wani irin tsoro da tashin hankali take jikinsa ya hau rawa yajata jikinsa ya k'ank'ame yace "ki kwantar da hankalinki Fatima babu abinda zai sameki da yardan ubangiji, Kuma ko wane tsinann ne ai yazama matsoraci tunda ya kasa tunkarana gaba da gaba yake bin dunduniyata.

Sosai ya rik'a bala'i yana masifa cikin wani irin mummunan b'acin rai, yayin da gwaggo tayita kukan tunawa da tilon 'yarta da kuma tausayin galin da d'an yayan nata yake.

Fatima kuwa bata runtsaba aranar da ta kwanta zakinnan zai zungureta yanayi mata kallon gargad'i.

Dole sai ad'akin suka kwana dukansu Abdul da gwaggon dan ma Allah yasa mijinta mai tafiyae tafiye ne.

Garin Allah kuwa yana wayewa ko karyawa Fatima  bata bari sunyiba tasa kuka tace ita ya mai da ita gida, lallashin duniya tace itafa batasan zance ba dan dole,sukayi gwaggo sallama suka

kamo hanyar gida.

Plss manage
Daga

Maman islam
[8/11, 7:49 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💧💦ZATO NE💧💦

NA

HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM

Daga marubuciyar
ABINDA YAKE RAINA
WAYYO RAYUWATA

......................kusan abinda yafaru a hanyar zuwan su shine yasake faruwa da k'yar Abdul majid yakawo kansa gida.

Cikin kwana d'ayannan da sukayi har Fatima tayi wata irin rama tayi wujiga wujiga da ita, abin tausayi duk ta wani firgice.

Lokacin da suka isa gida ana kiran sallahr azhar Ummi tana kicin ta had'a abincin rana taga giftawar Fatima da sauri.

Daganin yanayinta babu nutsuwa atattare da ita,da sauri Ummi tak'arasa abinda take tabi 'yar tata, saidai sanda tashiga d'akinnata har ta tayar da sallah, dan haka itama ta juya dan gabatar da tata sallar.

Ab'angaren Abdul ma yana shiga b'angarensa wanka yafarayi agaggauce sannan yayi alwala ya wuce masallaci.

Yana dawowa daga masallaci direct wajen mammy ya wuce , suna dirning area ita da autarta suna cin abinci.

Mammy tabi d'annata da kallo tana amsa sallamar dayayi memma tayi masa sannu da zuwa tanafad'in "nidama nasan Fatima bazata iya sati guda abajoga yadai fad'ane kawai.

Kallonta Abdul yayi yana tambayar ta da ido, wai yaushe akayi hakan?
Memma tace sanda kuke shirin tafiya tace min ita tanason ku d'an kwana biyu acan bayan tafiyar ku kuma naga message d'inta wai zata lallab'aka har kuyi sati"

Murmushi yasaki har saida kyawawan hak'oransa suka bayyana memma tasaki baki tana kallon yayan nata wani mashahurin kyau yake yi aduk lokacin da zaiyi dariya.

Gaida mammy yayi yana dungure kan meema yace"duk kin d'aukemin hankali da d'an banzan surutunki ko uwata ban gaisarba.

Dariya memma tayi kafin tace "wai ina Fatimanne yaua naganka kai kad'ai koda gaske ka barota acan d'in?"

Itama mammy kallonsa take tajiran jin amsar da zaibata, "ban saniba suda kinga k'yaleni yunwa nakeji mammy zubomin abincin dan Allah"

Mammy tace "bangane baka saniba inakabaromin yarinya?"

Ta masa tambayar tana tura masa flat d'in abincin data zubo masa, saida yayi bismillah yafara cin abincin dan yunwa yakeji sosai Fatima bata bari sunyi karin kumalloba ta uzzura masa suka taho.

Duban mammy yayi yace "tana fat d'insu dan ko kari bata bari munyiba tace ita gida zata tafi"

Nan kuma ya kwashe duk abinda yafaru a hanya ya fad'awa mammy, bak'aramin girgiza tayi dajin wannan abinba tabbas duk ma wanda yake bin baya d'annata baizai denaba ya zama dole ta fad'ima Abbu dan tasan tabbas zai iya bada taimakon daya kamata.

Abangaren Fatima,kuwa saida tayi sallah sannan tayi wanka,dake sanda ta shigo gidan anriga da antada sallah.

Bayan ta shirya cikin wasu riga da sket 'ya kanti kalar blue mai duhu sunyiwa jjar fatarta kyau sosai.

A falo tasami Umminta tana cin Abinci kusa da ummin ta zauna tagaida ita sannan taja abincin yayinda ummin take tambayarta yanda ta barosu.

Tace "duk suna lafiya ummi tace agaidaku, ummi ta d'an k'ara kallon 'yar tata da kyau ganin yadda ta zuk'e lokaci d'aya tace

"Ciwo kikayi ne adaren jiya naga kin zuk'e?"

Ajiyar zuciya Fatima tayi kafin ta dubi ummin da idanunta da har sun,ciko da kwalla take abinda yafaru yafara dawo mata kamar yanzune abin yake faruwa babu 'yar b'oye b'oye tsakainta da umminta take ta kwashe duk abinda faru ta fad'awa ummin, wanda itama ummin bak'aramin girgizata abin yayiba karfa kuma wani abu yasami tilon 'yar tata dan tanada kusanci da Abdul majid?

Ai kusancin su ba aure bane kuma ko Abdul majid yace yanasin Fatima,bazata tab'a amincewa ba dan,abinda ta lura dashi duk wanda zai mu 'amalance shi koda da soyayyane sunan shi gawa.
Wannan kenan

Ab'angaren mutuminnan kuwa tsaye yake gaban gunkiyar nan yau idanunta har ya wuce rannan haka duk wani k'ofa najikinsa babu inda baya kwarar dajini.

D'ago wutar dakeci a idaninta tayi naga ta kalli mutumin wanda duk ranar datayi hakan mutum ya b'ata mata rai kuma wannan kallon shima azaba ne dan mutum zaiji ajikinsa.

Jinai tana magana yau kuma da muryan jarirai tace "wayace kabita kanason lalatama aiki bakasan cewa idan ubanta yasan kana bin ta sai ya kawo k'arshenkaba? dan mudai munriga da munfi k'arfin duk wani mai shiri akanmu"

"Kar ka sake binta lokacin baiyiba idan lokacin yayi dakaina zan d'auko ta domin muna buk'atarta dan gudanar da wani gagarun shiri amma,ba yanzuba da sauran lokaci

Daga haka ta rufe idanun tana hawayen jini,alamun tagama,bayaninta.

Gani nayi wata irin iska tayi watsi dashi bai fad'i a ko inaba sai bakin falon gidansa, wannan shine hukuncin duk wanda ya sab'a umarninta

A sume yake tun bayan sa adda wannan aba ta watso shi bashi ya farkoba sai bayan da iskar asbah ya hurashi.

Da sauri ya tashi yashige d'akinsa duk jikinsa babu inda baya masa ciwo bin matarsa yai da kallo wadda bata san mai yake faruwa toilet ya shige yayi wanka da ruwa mai mugun zafi wai ko zaiji dad'in jikin sannan ya d'auro alwala yazo yatashi matarsa sannan shi kuma ya wuce masdalan
[8/11, 8:40 PM] MAMAN ISLAM: *بسم الله الرحمن الرحيم*

*☀️ FIRST CLASS WRITERS ASSOCIATION ☀️*

FCWA

*Home of qualities and trusted writers of the nation*

https://free.facebook.com/111719967001810/photos/a.111720050335135/116072649899875/?type=3&source=45&refid=17

---

💧💦ZATO NE💧💦

NA

HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN

BY
MAMAN ISLAM

Daga marubuciyar
ABINDA YAKE RAINA
WAYYO RAYUWATA

Page 7

......................kusan abinda yafaru a hanyar zuwan su shine yasake faruwa da k'yar Abdul majid yakawo kansa gida.

Cikin kwana d'ayannan da sukayi har Fatima tayi wata irin rama tayi wujiga wujiga da ita, abin tausayi duk ta wani firgice.

Lokacin da suka isa gida ana kiran sallahr azhar Ummi tana kicin ta had'a abincin rana taga giftawar Fatima da sauri.

Daganin yanayinta babu nutsuwa atattare da ita,da sauri Ummi tak'arasa abinda take tabi 'yar tata, saidai sanda tashiga d'akinnata har ta tayar da sallah, dan haka itama ta juya dan gabatar da tata sallar.

Ab'angaren Abdul ma yana shiga b'angarensa wanka yafarayi agaggauce sannan yayi alwala ya wuce masallaci.

Yana dawowa daga masallaci direct wajen mammy ya wuce , suna dirning area ita da autarta suna cin abinci.

Mammy tabi d'annata da kallo tana amsa sallamar dayayi memma tayi masa sannu da zuwa tanafad'in "nidama nasan Fatima bazata iya sati guda abajoga yadai fad'ane kawai.

Kallonta Abdul yayi yana tambayar ta da ido, wai yaushe akayi hakan?
Memma tace sanda kuke shirin tafiya tace min ita tanason ku d'an kwana biyu acan bayan

tafiyar ku kuma naga message d'inta wai zata lallab'aka har kuyi sati"

Murmushi yasaki har saida kyawawan hak'oransa suka bayyana memma tasaki baki tana kallon yayan nata wani mashahurin kyau yake yi aduk lokacin da zaiyi dariya.

Gaida mammy yayi yana dungure kan meema yace"duk kin d'aukemin hankali da d'an banzan surutunki ko uwata ban gaisarba.

Dariya memma tayi kafin tace "wai ina Fatimanne yaua naganka kai kad'ai koda gaske ka barota acan d'in?"

Itama mammy kallonsa take tajiran jin amsar da zaibata, "ban saniba suda kinga k'yaleni yunwa nakeji mammy zubomin abincin dan Allah"

Mammy tace "bangane baka saniba inakabaromin yarinya?"

Ta masa tambayar tana tura masa flat d'in abincin data zubo masa, saida yayi bismillah yafara cin abincin dan yunwa yakeji sosai Fatima bata bari sunyi karin kumalloba ta uzzura masa suka taho.

Duban mammy yayi yace "tana fat d'insu dan ko kari bata bari munyiba tace ita gida zata tafi"

Nan kuma ya kwashe duk abinda yafaru a hanya ya fad'awa mammy, bak'aramin girgiza tayi dajin wannan abinba tabbas duk ma wanda yake bin baya d'annata baizai denaba ya zama dole ta fad'ima Abbu dan tasan tabbas zai iya bada taimakon daya kamata.

Abangaren Fatima,kuwa saida tayi sallah sannan tayi wanka,dake sanda ta shigo gidan anriga da antada sallah.

Bayan ta shirya cikin wasu riga da sket 'ya kanti kalar blue mai duhu sunyiwa jjar fatarta kyau sosai.

A falo tasami Umminta tana cin Abinci kusa da ummin ta zauna tagaida ita sannan taja abincin yayinda ummin take tambayarta yanda ta barosu.

Tace "duk suna lafiya ummi tace agaidaku, ummi ta d'an k'ara kallon 'yar tata da kyau ganin yadda ta zuk'e lokaci d'aya tace

"Ciwo kikayi ne adaren jiya naga kin zuk'e?"

Ajiyar zuciya Fatima tayi kafin ta dubi ummin da idanunta da har sun,ciko da kwalla take abinda yafaru yafara dawo mata kamar yanzune abin yake faruwa babu 'yar b'oye b'oye tsakainta da umminta take ta kwashe duk abinda faru ta fad'awa ummin, wanda itama ummin bak'aramin girgizata abin yayiba karfa kuma wani abu yasami tilon 'yar tata dan tanada kusanci da Abdul majid?

Cikin sanyin jiki Amma tace "da ace babu wannan masifar to danafi kowa farin ciki kana kallofa Yusifa yadda Hafsatu tarasa tilon 'yarta k'wa d'aya tal aduniya, sannan kuma natar Ridwanu babu irin haukar dabatayi minba akan nace zan had'a 'yarta da shi Abdul majidun hakama danace a had'a da Nusaiba 'yar wajen Umaru shima wai kar ab'ata zumunci duk fa 'yan uwansa ma suna gudun abinda zai Faru shine Habu zai jawa kansa matsala da matarsa?"

"Gaskiya  Yusifa kace baka yardaba kawai fak'at nagama magana"

Daddy wanda jikinsa yqyi mugun sanyi yayi k'asa da kai yakasa cewa komai baitab'a sa abin aransaba irin yau da mahaifiyarsa ta ankarar dashi cewa 'yan uwansa ma gudun gudan jininsa sukeyi wanda da ace babu wannan matsalar da bak'aramin rigingimu za ayiba akan Abdul d'inba koba dan dukiyaauba ma kodan kyawun dayake dashi.

Haj. Kulu ce gurfane agaban bokanta datayi imani dashi akan duk wasu buk'atunta bayanin take masa akan matsalar da mijinta yake son bata akan maganar auren 'yarta da Abdul majid bokan kamar zaiyi kuka yace mata karki damu bama sai anyi wani aikin akansaba dole aurennan saiya faru dan haka kije kici gaba da shirinki aure yananan babu fashi.

Washe baki haj. Kulu tayi tace boka aikinka yana kyau shiyasa nake alfahari dakai nabaka dukkan yardata zip d'in jakarta ta bud'e taciro bandir d'in 'yan dubu na dubu d'ari ta zube agansa, kamar zaiyi kuka ya daki kud'in da sandar hannunsa suka b'ace zaki iya tafiya ya fad'a kamar zaiyi kuka.

Tana barin wajen suna zuwa mutumin ya dubi bokan yace "kai dan ubanka menace maka banace ka lalata maganar aurenba banace karka bari auren yafaruba"

Boka dayaji shaka yace "haba yallabai naga kafini k'arfi da fada awahen shugaba meyasa kai bazakasa ta hana aurenba saini k'aramin alhaki da ake bani dafa i'daga gefe zakabi ka

takurawa naso ace 'yar cik8nkace za ayi wannan auren da ita ba 'yar abokinkaba da ni dakaina zan tsotse jininta kamar yadda kayiwa tawa 'yar guda d'aya tal aduniya"

Wata irin bangaza mutumin yayi masa a firgice ya danganda wajen gunkiyarsu, sosai jikinsa yane b'ari ganin yanayin uwar gijiyar tasa yace "kimin rai ajanye maganar aurennan yarinyar nana 'yar amini nane wannan auren zai saka damuwa azuk'ata da yawa harda na mahaifiyar yarinyar.

Yauma kamar rannan naga ta bud'e idonta akansa, take jikinsa yafara wani irin rawa ganin yau wutar dake ci har yazarta k'aida tace "kayi tunanin yadda iyayen yara da 'yan mata ko 'ya'yan tsofaffi sukeji aduk sanda muka buk'aci wasu daga ciki kuma haka kake kawosu babu jinkiri ko b'ata lokaci, dan haka duk abinda nak'ara shimfid'wa ka k'ara nusawa jininka zamusha jininka zamusah" haka tayi ta nanatawa har ta rufe idanunta kirib kamar kullum jinin yaci gaba da fita ta kowace kafa ta jikinta.

Wani irin kuka yafashe dashi kuka harda majina fuskar nan yayi wani irinja jiki na rawa ya mik'e nan yabar takalmansa da jakarsa.

Sanda ya shiga gidansa matarsa bata gadon alamunta yaji a toilet da sauri ya cire kayan jikinsa ya canja wasu tana fitowa taganshi tace "daga ina kake alh.
Tun d'azu na farka nake ta nemanka?"

In ina yasoma yana share gumin daya lullub'eshi kafin yasami abinda zai fad'a mata dak'yar yace,

"Ajiya ce akabani ta miliyoyin kud'i na mantasu a mota shinefa hankalina kikaga yabar jikina"

Kamar bata yadda da abinda yace ba tace"oh to yanzun kaga kud'in kenan?"

"Na gansu" yafad'a yana goge gumin dayake ta kwaranyo masa gaba d'aya alamomin rashin

gaskiya sun bayyanar masa.

Tab'e baki matar tayi tace "ajuri zuwa rafi wataran tulu zai fashe duk abinda mutum zaiyi ya dinga duba Allah" daga haka ta wuce ta shimfid'a abin sallah.

A gidan su Abdul majid kuwa babu wanda ya goyu da bayan wannan had'in musamman umma matar baba Ridwanu babar Nusaiba k'iri k'iri ta nuna batason wannan had'in.

Shi kuwa Abbi tunda yasamu yashawo kan yayansa da uwarsa shikenan aka wuce wajen babu wanda ya saurara da shirmansu.

Ko uwar yarinyar take ta rigingimu da koke koke bai sauraretaba tayi kukan tayi rok'on tayi magiyar duk abanza yak'i sauraronta.

Fatima kuwa tunda ga ranan bata k'ara samun lafiya ba kullum suna hanyar asbiti abinda ya dad'a d'aga hankalin ummi kenan kullum saita yiwa Abbi tana rok'onsa akan ya janye wannan batun amma ko kallon inda take.

Sai dai kuma tunda yai mata rubutu yabata ta sha bata k'ara wannan mugun zazzab'inba sannan kasshi saba in daga d'ari na tsoron daji aranta ta nemashi ta rasa dan haka tareda itama ake rarraahin umminta da duk tabi ta rame sai uban hanci zuwait.

Yauma kamar rannan zaune suke a d'akin na musamman wanda ya kasance wajen mihimmin tattaunawa agareau duk dai akan batun na Abubakar wanda baima sanda shirinsuba amma yana nasa shirin.

Abdul majid tun ranan da Abbi ya yanke wannan shawaran bai k'ara sanya Fatima a idonsaba sai yau ya hango ta a wajen aje motoci da alama fita zasuyi ita da meema ne, wajen ya nuga.

Meema ce ta d'an zunguro Fatima wacce hankalinta yana kan wayar da sukeyi da k'awarta tacan misra Rasheedat A maleek ta nuna matashi take idanunsu ya sark'e cikin na juna suna,kallon junansu da irin ramar da dukansu sukayi.

K'arasawa yayi wajen yana kallonta ko k'ibtawa bayayi, yayinda itama take kallonsa hannunta kamo ya zare mukullin motar kafin ya juya wajen Meema yace "ina zakujene bana hanaku fita da mota natareda driver ba?" Meema tad'an had'e rai tace "Abbinefa ya aikemu gidan sheik Aminullah"

Cikin sanyi yace "to muje nakaiku ko"

Babu musu Meema ta bud'e bayan tashiga dan dole ta shiga gaban motar ya tadata suka,fita.

Saida suka d'an yi tafiya mai d'an nisa kafin  ya dubeta yace "Fatima banji kince komaiba akan hukuncin da iyayenmu suka yanke"

Dubansa tayi da idanunta har sun d'anyi ja tace "me kake so nace yaya sokake nace maka ban aminceba kome?
So kake na tsallake maganar Abbina?
Sam ban sami irin wannan tarbiyar daga ummi ba ta musu da iyayena komai sukace haka zanyi koda kuwa hakan yana nufin ajalina dan haka ZAN AUREKA YAYANA.

Dubanta yake da mamaki yace "Fatima kin manta da damuwana ne kike son jefa kanki a halaka?"

Tace "to yaya kake so nayine yayana kasan idan Abbi ya fad'i abu zaiyi wahalan gaske ya canja dan haka NI NA DOGARA GA ALLAH KUMA INA NEMAN SAUK'I DAGA WAJENSA"

Muje zuwa taku yar mutan yakasai

Maman islam
[10/7, 5:03 PM] Maman Islam: بسم الله الرحمن الر حيم
*___________________________________*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*_____________________________________*

💦💧ZATO NE💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI
WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM

Page 13

......................da sauri Fatima ta d'auke kanta daga kallon da taiwa Yusra guda d'aya tak saboda 'yar iskar riga da tasaka marabanta da tsirara kad'anne.

Cikin rausaya tafara takowa tana girgiza jiki, yayinda Abdul ya k'araso kansu ta tsaya tana musu wani d'an iskan kallo kafin ta wani juya ido tace

"Me zan gani Abdulmajid wannan ai bayi bane akan me zakanganka anan"

Kallinta yake da son k'arin bayani yayinda Fatima tayi masifar had'e rai ta maida kanta gefe.

Ita kuwa Yusra cigaba tayi da fad'in "kaifa mukayi dakai nice uwar gidanka ya kuma zanganka anan wannan ai ba adalci bane"

Kallonya yake da mamakinta kafin yace

"Ni kikayi dani nace miki hakan yaushe mukayi haka dake dazakizo min da wannan banzan shirmen?"

Zama tayi ajikinsa tana wani shafashi ko kunyar idon Fatima babu yayin da Fatima ta fusata tabar wajen afusace, wani kallon gefen ido Yusra tabi Fatima dashi tareda sakin wani shu'umin murmushi, sannan tace

"Haba dear nicefa gaba da Fatima gaakiya ban amince wacca yarinyar ta jagoranceni amatsayin uwar gidana dan haka ban yardar maka ka kwana ad'akintaba haba ai wannan siyawa mutum rainine"

"Sannu uwata cewar Abdulmaji tsakanin ke da Fatima auren wa akafara d'aurawa? dazaki

zomin da wani banzan shirmanki, to inaso kisan cewa ko a addini Fatima ce uwar gidana tunda saida aka fara aurenta kafinnaki, inafatan kin gane ko?"

Ran yusra in yayi dubu to yab'aci saboda maganganun da yafad'a, ta had'e rai tace "ai wannan zaluncine dama kasan abinda ka shirya shiyasa zaka maida wannan tsigag".....ke Abdul ya buga mata tsawa yace

"Karki sake kizagar min Fatima idan kuwa ba hakaba wallahi zan baki mamaki"

Ta wani murgud'a baki tace "idan anzageta mezakayi tsabar rashin adalci daga kawoni jiya jiya har zakafara nuna rashin adalci to wallahi babu wanda ya isa ya tauye min hak'k'i na zuba ido ina kallo, daga haka ta bar wajen afusace.

Girgiza kai yayi yabi Fatima sama lokacin har tagama shirin bacci har lokacin ranta ab'ace yake da abinda Yusra tayi mata.

A hankali ya murd'a k'ofar ya shigo a nutse ya tako ya iso inda take kallo d'aya tamasa ta d'auke kanta tayi kwanciyarta

Murmushi yayi yak'arasa kusa da ita ya zauna yana kallonta yace"babyna me yafarune naga kina ta hararan gefe"

Turo baki tayi batareda tace masa komaiba tana k'ok'arin juya masa baya ya rik'eta yana kallonta.

Itama kallinsa take kafin ta wani had'e rai tace "katashi kaje wajen matarka uwar gida kartaga ka shiga hak'k'inta"

Kallonta yake da mamaki kafin yace "wace matar bayan wadda nake tareda ita ayanzun? Kuma dazakice haka wa aka fara kawomin dan haka ke zan fara dake kafin wata kingane ai"

Yafad'a da sigar tsokana, jitai gabanta yafad'i tace "ni na yafe mata kaje can d'in kawai"

"Baki isaba wallahi babyna dan haka karki k'ara magana daga haka ya jata jikinsa yana mata wani irin salo wanda take ya rikitata.

Sosai jikinta yafara rawa jin wani irin bak'on al'amari sosai yashiga sarrafata shima dayake abin bak'one awajensa babu inada baya rawa ajikinsa.

Tuni yagama fita a hayyacinsa yasoma wasu surutai marasa kan gado, da k'yar yasamu ya iya kashe fitilan d'akin kafin yashiga raya daren.

Sosai Fatima taci bak'ar wuya a hannunsa abinkada ba sabanba, saida ya samu gamsuwa sosai sannan ya ja mayafi yarufesu tana jikinsa ya kunna fitalan d'akin haske ya gauraye d'akin gaba d'aya Fatima ta d'an bud'e idobta kad'an me zata gani akusa da ita?
Ai wani irin razanannen ihu tasaka sannan ta k'ank'ame Abdulmajid jikinta na wani irin rawa sannan kuma ta sume.

Kwance take tana bacci amma sai faman juya kanta take ga uban gumin daya jik'ata sharkab, yayin da yaga haka sai ya kama mata tofi dama tun d'azu daya tashi bai komaba daidai lokacin yake gabatar da duk abinda zaiyi na ibada.

Wata irin zabura tayi kafin tamik'e zaune tana salati tace "wayyo Abbi na shiga uku zasu kashe mana Fatima ka taimaka mata karsu kasheta"

Jikinta babu inda baya rawa tsabar firgici da tsoratan datayi gaba d'aya tagama fita a hayyacinta da k'arfi Abbi ya rik'eta yana cigaba da tofa mata addu'a har saida tadawo nutsuwarta kafin ya dubeta yace

"Yakamata idan zaku kwanta bacci ku dinga addu'a kodan mugayen mafarkai yanzun sai shaid'anu suyi galaba akanka"

Fashewa tayi da kuka tace "Abbi dan Allah kiramin Fatima wallahi sunbita karsu rabamu da 'yarmu Abbi"

Tafad'a cikin fashewa da matsanancin, kuka kallonta Abbi yake da mamaki yace "haba Ummusalma duk kinbi kin rikitani meya sami Fatiman yarinyar da d'azu inajinki kuna hiranta da meema har kina tambayar yadda suka barota ta tabbatar miki da lafiya lau take"

"Allah Abbi shigaban qungiyar 'yanshan jinine yaje gidanta yana can kuma ka kira Abdulmajid katambayeshi"

Da mad'aukakin mamaki yake kallonta kafin yace "waye yafad'a miki ummu?

Cikin kuka tace "gani nayifa amafarkina sun zagayesu daga ita har Abdul d'in suna k'ok'arin tab'asu"

Wani mugun tsaki Abbi yaja sannan yace "wallahi Ummu bantab'a sanin cewa kin samu matsalan k'wak'walwa ba sai yau, ke yanzun banda shirmenki da abinda kika gani amafarki kike gasgatawa?"

"Tabbas wani mafarkin yakan kasance gaskiya amma ke kam naki damuwan da kikasa arankine kuma kika kwanta bakiyi addu'a ba"

Da k'yar yasamu ya lallabata itama tayo alwala tazo ta kabbara sallah.

Amugun firgice yake jijjigata yana tambayar abinda yasameta wanda batasan yanayiba, sosai ya rikice yakama hawaye yana surutai shikad'ai wanda ma baisan abinda yake fad'aba.

Yajima yana kuka kafin yayi dabarar zuwa ya had'a ruwan wanka ya tsarkake jikinsa sannan itama yazo ya d'auketa ya sakata a ruwan wata irin ajiyar zuciya ta sauke da k'arfin gaske kafin ta fara fisge fisge tana surutai.

Menayi muku me mukayi muku kuke binmu dan Allah kuyi hak'uri ku k'yalemu muyi rayuwarmu me kukeso me kuke nema awajenmu.

Sosai take surutai da k'yar yasamu ya gama mata wankan sai dai babu damar tsarkake mata jikinta tunda dole sai tayi niyya dan haka ya nad'ota atawul yadawo da ita d'akin yana cigaba da tofa mata duk addu'ar datazo bakinsa

Plss manage

Taku maman islam
[10/7, 5:03 PM] Maman Islam: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*__________________________________________*

Gaskiya inaji da ku masoya ina mutukar alfaharida ku,
Ammin sadik
Ummu thurab
Adama Aliyu
Bint muhammad
Maman meemat
Tareda sauran wanda ban ambataba ina godiya kwarai Allah yabar kauna bisabilillah

Ummukhaleel alherin Allah ya isar miki aduk inda kike ina gaidake tareda khaleel da khairat

My princess yakike ya rikici gaskiya tsufa yasakaki rikici dayawa princess Aishatu
Allah yabar zumunci

💦💧ZATO NE💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM
DAGA MARUBUCIYAR.

ABINDA YAKE RAINA
WAYYO RAYUWATA

Page 11

..................wata irin ajiyan zuciya ya sauke kafin yace "shikenan Fatima tunda kikace haka amma fa inaso kisani daga yau baccinki ya k'are baki da wata nutsuwa tunda kika amince da wannan auren to wallahi babu ke babu ke babu farin ciki.

"Humm yaya kenan ba'ace zan aurekaba ana bina ana firgitani bare yanzun,kuma nafika sanin wannan kuma nagama yarda ni yanzune ma nafarjin duk duniya babu wanda yakaini k'aguwa ayi auren dan haka kasa aranka cewa Fatima bata maka so irin na aure amma zata aureka dan haka karka wani damu zanga tsinannen daya hanaka samun salama arayuwarka"

Daga haka bata k'ara cewa komaiba ya taida idonta kan hanya.

Shiko bansan mai yasaba sai yaji sam baiji dad'in kalmarta ta BANA MAKA SON IRIN NA AURE.

Wannan kalma yaji d'acinta ba kad'anba kallonta kawai yake yakasa d'auke idanunsa akanta shi yarinyarma duka mamaki take bashi yanzunefa take shiga shekara 17 amma take iya fad'a masa wannan maganar agaskiya abin ya masa ciwo.

Har sukaje suka dawo babu wanda ya kuma tankawa d'an uwansa sanda sukayi perking har ta kama k'ofar zata bud'e yace "bakijiba" fasa bud'ewar tayi ta gyara zamanta yayin da tuni meema ta wuce abinta.

Dubanta yake da mamakin yadda take ta wani cin magani wani murmushi yayi mai ciwo sannan yace.

"Wane shirin kukeyi ne kinga abin yana ta matsowa dan haka kiyi maganar abinda kuke da buk'ata kafin lokaci ya k'ure "

Kallonsa tayi kafin tasaki wani malalacin murmushi tace "yaya kenan wane shirine ga mutumin da k'afarsa d'aya take alahira d'aya a duniya?
Ai kawai ina ganin kafara lissafin sauran rayuwar data ragewa Fatima aduniya bawai wani shagaliba, nifa wannan auren zanyi shine kawai dannasan yazama dole ayishi tunda mahaifina ya furta amma badan hakaba idan ka tona,zuciyata kamar gawayi take saboda tsabar yadda nake k'in abinnan araina"

Kallonta kawai yake zuciyarsa na masa wani irin suya shine yau Fatima take gasawa magana irin haka I?
Lallai duniya nakama kenan saboda wata lalura ta sameka shima yana gudunka ina kuma ga bare wanda bai had'a komai dashiba.

Yana kallo har ta bud'e motar ta fice bai iya k'ara cemata komaiba.

Tana shiga falonsu ummi ta kirata tareda mika mata wani rubutu a d'aure aleda tace "kiyi bismillah kisha daga tsaye sannan ki wuce kiyi alwala kizo kiyi sallah Abbin ki yace yau k'arfe uku me miki gyran jiki zatazo"

K'ure ummin tayi da ido saisai zuciyarta na bugawa kafin tace "ummi nifa babu wani shiri da zanyi auren da babu wata soyayya acikinshi ta ina zaiyi armashi?"

Ummi tace"ai kuwa gyara ya zama dole Fatima kowace amarya ko ta wasan yarace ana gyarata bare kuma ta d'an mutum dan haka kawai kije kiyi abinda nasakaki"

Jiki a sanyaye ta sha rubutun ta wuce d'akinta.

Umma ce da Anty Ruk'ayya zaune afalon umma Anty Ruk'ayyance ta dubi umma tace"  kinga irin abinda nake fad'a miki ?ko dama saida nace miki may be idan aka had'ashi da yaran gidannan babu abinda zai faru kik'i yarda kikace ke ba hakaba yanzu gashi za'ahad'ashi da wannan nunar ranan kuma shiru kakeji babu wani alamu na tashin hankali atareda su yanzu gashi munaji muna gani wannan dukiyar zaiyi mana nisa"

Umma tace " ke dalla malama ki rufemin wannan k'azamin bakinnaki anan ke k'aramar yarinyace da bakisan komaiba, ina so ki bud'e idonki sannan ki kasa kunnenki kiga abinda zai faru idan anyi auren an fad'a miki wanine daban yake bin Abdul majid? to shida kansa yake shanye jinin duk yarinyar dayake nema,ance miki wannan dukiyar nasu na banzane idan kuma ba hakaba ai akwai baby meyasa baki bashi itaba ainagama ta girmi Fatima.

Anty Rukayya data gama tsorata tace "a a umma ai bansan haka abin yakeba wallahi nidai babu ruwana dan Allah mubar maganar iya nan"

Wani muemushin samun nasara umma tayi sannan tace"to dama Rukayya ai wannan ba maganar yad'awa bace amma kisa ido sosai zakiga abinda nake fad'a miki"

Sosai anty Ruk'ayya ta tsorata jiki na tsuma tafice daga sashin umma, yayin da umman tabita da wani kallo tana wani shu'umin murmushi.

"Alh na fad'a maka yadda ka lalata maganar nan maza kaje ka gyarata da kanka kabasu hak'uri sannan ka tabbatar musu da cewa maganar aure tanan kamar yadda aka tsaida ita"

Dubanta alh yayi yace "dan Allah haj kibar maganar nan alh Galinefa yacemin yaron d'an mafiyane kuma yace shi da kansa yake tsotse jinin,duk matar da ya nema da nufin aurenta"

Wani banzan kallo naga haj. Kulu tanayiwa alh, kafin tace "shi alh, Ghalin indai batare suke hark'allar da yaronba ta ina yasan wani Abdul majid bare yasan cewa shi d'an mafiyane zaka tashi kaje kanemi afuwarsa asasanta maganar ko saina yimaka rashin mutunci"

Jiki na rawa alh. Sambo ya mik'e yana fad'in " yadda kikeso haka za'ayi hajiya bari naje na isar da sak'nki"

"Kuma kwantar dakai zakayi ka nemi afuwarsu karka sake naganka anan batareda ka daidaita komaiba"

Yace "angama hajiyata"
Daga haka ya fita cikin takaicin yadda haj take masa wanda Allah ya jarabceshi da tsananin tsoronta.

Agidan Alh. Yusif kuwa da k'yar suka hak'ura da batun dan harda kuka saida alh. Sambo yayi dan yana tsoron masifar haj. Kulu matuk'ar ya koma mata batareda an sasanta wannan maganar ba.

Saida Amma da Abbi suka sa baki anan Abbi yake sanar musu da cewa yayi istuhara aurennan shima dole ayi dan haka kawai su hak'ura kawai a had'a dana Fatima.

Gidan alh. Sambo kuwa yana fita naga wannan mutumin mai zuwa wajen gunki ya ahigo gidan bak'aramin jijjiga nayi daganinsaba araina nace meye to had'insa da alh. Sambo kodai da gaske alh. Sambo abokinsa ne ko kuma tare suke k'ulla hark'allar tasu?

Wani irin ciza na gantsarawa yatsana ganin har sun gama maganarsu da haj. Kulu yafito batareda na saurari maganar da suka tattanaunaba ina can shashancin tunanin abinda ya kawoshi.

Bayan sati d'aya, sosai Fatima tayi wani irin fitinannen kyau naga tayi saikayi dagaske zaka ganeta saboda yadda gyaran ya amsheta gaba d'aya ta canja.

Su meema,kuwa shiri suke sosai duk dacewa har lokacin jikin iyayen angon asake saboda tsoron abinda zaije yazo wannan ne karon farko daza afara aurar da yaran gidan duk da kasancewar ayanzu Abdul majid yana da shekara talatin da uku cif aduniya.

Ab'angaren Yusra kuwa rankai ba magana sosai take shiri domin ba k'aramin so takewa Abdul majid ba tana sane sarai dacewa bin na mutum biyune tabar hakan a zuwan saita shiga gidan zata d'auki mataki kuma tasanarwa Abdul majid cewa yazama dole ta kasance a uwar gida tunda itace yafara cewa yana so.

Shi kam sanda take wannan batun murmushi kawai yayi dan ya riga yagama yankewa waye uwar gida waye kuma amarya.

Yauma bai yardaba ya kuma komawa wajen boka duba yace "bikin 'yar abokina sai dad'a matsiwa yake nace ka dakatar kak'i ko?
Wallahi duna zanyi maganinka ne"

Wata irin dariya naga bokan ya shek'e sannan yace "Ak'ilu kenan ai yanzun wuyana yayi kauri na wuce tunaninka nayi k'arfin dabaka isa kaja daniba idan kuma kana da ja bismillah, kai banda kai wawane kayimin sanadin tilon 'yata kayi tunanin zan k'yakeka?
Ina nan shirin ta yadda zanyi maganinka lokaci guda kai kana gudun akashe 'yar abokinka wanda azahiri ninasan dalilinka akan hakan ka zuga uban 'yar kuma sai akayi dace shid'in lusarin na mijne, mijin hajiya ko?inanan dawowa kanka" boka yafad'a dawata irinkakkausar murya ya b'ace ba't yabar alh. Ak'ilu da kuka wiwi da idonsa,

Muje zuwa

[10/7, 5:03 PM] Maman Islam: بسم الله الرحمن الر حيم
*______________________________________*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________________*

💦💧ZATO NE💧💦
NA

HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI

WRITTEN
BY

MANA ISLAM

Page 12

.....................yajima sosai awajen cikin tashin hankali sosai yaci kukansa ya godewa Allah sannan ya mik'e ya nufi gidansa firkai firkai dashi.

Lokacin da yashiga hidan matarsa tana saman kujera hankali kwance tana cin fruet bazaka tab'a gane yanayin da take ciki na dad' ko rashinsa, ganin yanayin da mai gidan ya shigo matane hankali atashe ta wani tab'e baki tacigaba da abinda takeyi.

Shi kuwa bai kula ma da ita awajenba ya wuce mugun sauri kamar zai tashi sama ya bud'e d'akinsa ya maida taciki ya rufe da key jab'ar yayi abakin gado yana kuka wurjanjan kamar wani

k'aramin yaro.

Can kuma kamar wanda aka tsikara naga yayi wani irin tashi tsaye ya nufi gadonsa a haukace yafara sauke katifar saman gadon sannan ya d'age karagar ya d'age capet saiga wata 'yar kofa ta bayyana kamar rijiya yana 'bude k'ofar ashe matattakalane aciki, kawai ya shige ciki da mugun sauri.

Abdul ne zaune a office d'insa babu abinda yake damunsa sai irin maganganun da Fatima ta gaggasa masa wanda bai tab'a damuwa da al'amarin waniba sai ita kwarai abin yatsaye masa arai.

Mammy kuwa da kanta ta d'auki wata shak'ik'iyar k'awarta suka had'o lefe na gani abada labari kayane masu matuk'ar kyau da tsada duka su biyun akwatuna sha biyu akayi musu saidai kayan Fatima sunfi na Yusra yawa.

Sosai ummi take taya mai gyaran jiki kula da 'yarta gashi ta b'angaren malam ma,ba azaune yakeba kusan zan iya cewama bashi da lokacin kansa saboda yadda ya maida hankali wajen son ganin yakamo bakin zaren abun.

Ab'angaren Yusra kuwa kanta ba k'ramin rawa yakeba shiri take sosai na bikin fati kusan kala hud'u tq shirya wanda Abdul ya tabbatar mata da babu d'aya da zai hallata.

Haka dai biki yacigaba da matsowa duka b'angarorin biyu sunata shirye shirye yayin da d'aya b'angaren basu da nutsuwa ko ta sisin kwabo domin bazasu manta da Salma ba d'iyar gwaggo Hafsatu wacce itace mace ta k'arshe da suka kasge shekara biyu daya wuce kisan wulak'anci sukayi mata kisan gilla domin gunduwa gunduwa sukayi da gab'ob'inta a tsakiyar gadon mahaifiyarta abinda ya girgiza familynta wanda shi kansa Abdul saida yafi watq agqdon asbiti domin har ga Allah yana mutuk'ar son Salma saboda itad'in mutum ce mai shiga rai saboda mutuk'ar hak'urinta da hankalinta.

Ab'angaren su umma da anty Rukaiyya kuwa tun ranan da umma,tace mata Abdul da ubansa ne suke kashe 'ya'yan mutane dan zalunci yaran da basujiba basu ganiba tayi mugun saka ido akan takun kowa nagidan duk abinda taga bai mataba take yi mugun sa ido akai.

Meema ce ta ahigo b'angaren ummi cikin kwalliya sosai da alama wani wajen zataje, afalon k'asa tasami ummi tana sharan falon tace "ummi ina Fatima take?"

Ummi tace " humm 'yar rigimana zakice yanzun muka gama da ita akan shan magani ayi yarinya bata k'aunar magani kwata kwata"

"Bata da lafiya ne?"

"Tun jiya take fama da ciwon kai jiya da darema saida mukaje asbiti"

Da gudu meema ta haye saman, akwance tasameta asaman gado tana wani irin juyi asaman gadon kanne yayi mugun matsanta mata.

Da sauri meema tak'arasa kusa da ita ta rik'ota hankali tashe tace "dear me yake damunki haka?"

Da k'yar Fatima ta d'ago kanta ta dubi meema tace "dear kije Abbi yana d'akinsa dan Allah kice yabaki wannan man zan shafa kaina cirewa zaiyi wayyo,Allahna"

Ai da gudu meema tayi d'akin Abbi ta karb'o man tazo tad'agota jikinta ta hau shafa mata man agoshi tanayi tanayi mata tofin addu'o'i ganin yadda take zabura.

Cikin irin yanayin aka shiga shagalin biki wanda kafin lokacin saida akakai Fatima,asbiti kusan sau uku bareda Abbi yq bari mahaifiyarsa ko 'yan uwansa sun saniba.

Ansha shagali sosai duk da cewa Fatima daurewa kawai take kamar babu abinda yake damunsu suka gudanar da shirye shiryensu taro yawatse lafiya

Ranan juma'a akakai Fatima yayinda sai ranan asabar akakai Yusra wannan kuma duk tsarin angone.

Dake tare suka kwana da su meema,koda wasa bataga k'eyar angonba kuma hakan bai dametaba sosai su meema da su husna 'yan uwanta suka d'ebe mata kewa.

Abdul majid kuwa duk abinda yake faruwa agidan bai saniba saboda baima je gidanba tunda aka kai amaryar hankalinsa a mutuk'ar tashe yake saboda tsoron abinda zaije ya dawo.

Yaune karo na farko da aka k'addamar da bikin aurensa har amarya ta tare agidansa batareda wani abu yasametaba duk da cewa itama d'in bawai sun k'yaletaba ne yasani sarai akwai shirin da koma waye meson ganin ya kassara masa rayuwa.

Sosai abin yake damunsa yarasa ta yadda zai fara abin har yanzu Jamil baizo ba Jamil wani abokinsa ne wanda tare sukayi karatun gaba da primary sosai Abdul suka shak'u da Jamil wanda har yakai gidajen biyu suna zumunci adalilin abotarsu.

Cikin yaran da suka mutu akwai k'anwar Jamil Zulaihat wanda itama bak'aramin tashin hankali daginta suka shiga ba domin Zulaihat salihar mace ce

Kwance take saman gadonta tana kallon saman sillin tunanin yadda zata b'ullowa al'amarin takeyi idan taga kamar cewa ta samo mafita sai komai ya wargaje tarasa wane bakin zata kama daga cikin zarurrukan datake kullawa aninne yake neman zarta tunaninta.

Itama Yusra saida nata dangin suka kwana dan haka suma sai lahadi aukabar gidan tareda su meema gaba d'aya.

Zaune take gefen gadonta zuciyarta na wani irin bugu sai faman murzar hannunta da yasha jan

lalle shar dashi take duk da kasancewar tanajin zafin yadda take murza hannun amna bata fasaba yayin da zuciyarta yake wani irin bugu jikinta yake karkarwa.

Batasan da me zata faraba batasan abinda zai faruba shin da gaskene bin matan da Abdul majid yake aure ake ana kashewa ko kuwa wa'adinsune yayii?

Wannan sune tambayoyin data kewa kanta wanda amsarsu ya gagareta

Wannan shine abinda ayanzu ya zauna zuciyar Fatima takasa cireshi takasa samun koda meema ce suyi shawara akan hakan domin Abbi yace wannan sirrintane tabarshi tsakaninta da mahaliccinta da sannu Allah zai yaye mata hijabin dake tsakaninsu.

K'amshin turarensa ne yayi mata sallama tayi saurin d'agowa tareda lumshe idanunta saboda wani irin bugu da zuciyarta yakamayi da mugun gudu tayi saurin maida kanta k'asa tana sauke b'oyayyar ajiyar zuciya.

Kusa da ita ya zauna yakamo hannunta ya rik'e anasa yana so su had'a ido tak'i bashi damar hakan ya d'an lek'a fuskarta ba k'aramin fad'uwa gansa yayiba ganin yadda idanunta sukayi wani irin ja.

Hannu yasa ya kamo fuskarta ya tsura mata ido kusan minti biyu ta lumshe ido ta bud'e hawayen datake ta k'ok'arin dannewa suka sulalo cikin rashin jin dad'i yace" Allah yasa bagani nane yab'ata miki raiba har kikemin asarar tsadaddun hawaye"

Jasa kallonsa tayi zuciyarta har lokacin bai daina dukan,tara taraba sosai taji tsoron kusancinta dashi ayau.

Kafin ta ankare ya had'e bakinsu waje d'aya yana mata light kiss sosai jikinta ya kama wata irin

rawa take hawaye ya zubo mata.

K'aran bud'e kofar ne ya k'waceta daga hannunshi, gaba d'aya suka maida hankalinsu bakin k'ofar Yusrace tsaye sanye.

Kash kuyi afuwa yauma saida muka koma asbitin yasin😌😌
[10/7, 5:03 PM] Maman Islam: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*__________________________________________*

💦💧ZATO NE💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI
WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM
DAGA MARUBUCIYAR
ABINDA YAKE RAINA
WAYYO RAYUWATA

Page 14

Koda ta bud'e idanunta da salati ta bud'e tana sambatu, sosai hankalin Abdulmajid yatashi ransa inyayi dubu babu wanda bai tashiba bai san lokacin dayasoma zubda hawayen bak'in cikiba.

Shikam yaga ta kansa sai kace akan danginsa aka fara kud'i duk abin anhana shi samun nitsuwa da kwanciyar hankali dazaiga waye yake masa wannan masifar da da hannunsa zai kasheshi.

Fatima tana bud'e ido ta ganshi a zaune kusa da ita tafad'a jikinshi ta k'ank'ameshi tafashe da wani irin kuka, shiru yayi tareda dad'a janta cikin jikinshi zuciyarshi na masa wani irin rad'd'i shi kansa dazai samu yayi kukan dayasami saukin wani damuwar.

Mammy ta dubi Daddy tace "alh, yakamata fa mutashi tsaye akan yaronnan kar ciwonsa kuma yazo yatshi kuma mushiga uku"

Daddy ya dubeta cikin tsantsar damuwa yace "haka Amma tace min wai yazo tunda sassfe dad'a figewa adare d'aya tak ni narasa yadda zanyi da wannan masifar wallahi hajiya duk wanda na samu da hannu acikin wannan al'amarin bazan saurara masaba ko waye.

Mammy tace "wallahi algaji yadda ya shigo nima ba k'aramin tsoratani yayiba harfa kuka yayi anan wajen" tafad'a tana nuna inda yatashin da hannunta.

A firgice daddy ya dubeta yace "kuka dai haj, shi Abdulmajid d'in?"

"Tusawa kake alh, yaronnan yana cikin damuwa sosai ni yanzu sonake duk wanda yake da hannu acilin wannan tashin hankalin da muke ciki naganshi da idona dakaina zan d'auki mataki akansa wallahi"

Daddy ya kalketa kawai batareda ya iya maganaba saboda gaba d'aya abin yafara fin k'arfinsa har cid yasaka ab'oye a dinga bin bayan duk wani takun Abdulmajid da duk wani wanda yake mu'a malanta amma babu wani labari.

Shin suwaye? me sukayi musu? me suke nema awajensu dazasu gigita rayuwarsu dana yaronsu haka kawai?

Mik'ewa yai yafita batareda yacewa mammyn komaiba yayn data saki baki tabishi da kallon mamaki.

"Ak'ilu zaka mutu zaka murufa akan wannan shed'aniyar yarinyar yawan binta dakake yawan binta da kakevyawan azabar da wannan tsinannen uban nata yake ganamin domin babu wanda yasani dabk'asar k'afarka yake amfani idan kuwa baka rabuda itaba dakaina zan tsotse jininka na huta da bala'inka"

A mutuk'ar firgice alh, Ak'ilu yace "kiyi hakk'uri kimin rai bansan wannan kangararren mutunin ya ganomuba amma na miki alk'awarin sai kinsha jinin Abubakar da 'yarsa"

Wata irin tsawa ta buga masa tace "jinin Abunakar ai gubane bazai tab'a shanyuwa agaremuba saidai na 'yar tasa Fatima itama kuma bada k'aramin shiriba kabari tasamu ciki sai kafad'amin da wannan raunin na mai ciki zamu ci galaban saceta muyi yadda muka ga dama da ita dan haka kabar aikin kawai a hannunaaaaaa"kirib ta maida idanun ta rufe kamar kullum jini na malala daga idanun kamar hawaye.

Shiko Alh, ak'ilu yabaro wajenne da k'udurin babu shegen da ya isa yasha jinin Abubakar da 'yarsa Fatima inba shiba dan haka ko za amutu wallahi babu wanda zai d'agawa k'afa akan jinin Fatima da ubanta.

Tundaga wannan ranan babu wani abu daya kuma firgita Fatima domin tundaga lokacin bata k'ara ganin wani abin tsoroba yayin da basuyi sanua wajen addu'a ba kullum zasu gudanar da rayuwarsu mai kyau da tsabta sannan suzo su kimtsa kansu kuma sukama na filfili cikin

kwanaki bakwan da yaiwa Fatima har wani k'iba yayi saboda kulawan dayake samu daga gareta.

Ranan da ya koma d'akin Yusra kuwa yaga iyayi da rawan kai dan ita ko irin d'an jan ajinnan irin na amare babu ta dinga wani shige masa.

Yasha mamakin daya sameta a cikakkiyar budurwa yanda take  rawar kannan saidai kuma hakan yasanya kimarta mai girma a idonsa.

Haka suka cigaba da zama cikin kwanciyar hankali sai dai abinda yavlura dashi Yusra tana da yawan k'orafi dakai k'ara abinda bai tab'a samu daga Fatimaba ko da wasa.

Watan su uku Yusra ta samu ciki mai azaban laulayi kullim babu lafiya tana kwance abinda yasa Fatima ta d'auki dukan kulawarta ta maida kan Yuran duk abinda takeso jiki yana rawa Fatima zata dafo mata.

Da farko ma da gayya zatace tana son abu idan tavkawo mata saitace bataji bane bashi taceba kaza tace, haka baiwar Allahn zatayo abinda tace d'in ganin duk abinda tasata bata damuea yasa ta watsar da komai suke zamansu lafiya.

Sosai hankalin Abdulmajid ya kwanta dan ganin yadda matannasa suka had'e kansu.

Zaune suke afalon k'asa yainda Yusra take zaune saman doguwar kujerar Fatima kuma tana kai akwance kanta saman cinyar Yusra hira suke tanama Fatiman tsifar kai a haka haj. Kulu tayi sallama da sauri Fatima ta mik'e tana mata sannu da zuwa, ta shiga kicin takawo mata ruwa da lemo, tadurk'usa har k'asa ta gaida ita cikin sakin fuska ta amsa mata tareda tambayarta yadda suke tace suna lafita daga haka ta mik'e ta haye sama tabasu waje su gana

Haj. Kulu wata irin macece mai jarababben son kud'I ita dai indai zata samu kud'I ko boka da 'yan bori bazata biba ganin yadda Abdulmajid yake sakar musu kud'in kamar baisan zafin

nemaba yasa sam bata wani damu da neman wani tenako wa Yusaran ba akan zannasu.

Sannan kuma Fatima bata da mugunta ko kad'an duk abinda Abdulmajid zaiwa Yusra bata da damuwa tunda itama babu abinda ta nema tarasa hasalima indai maganar kud'ine batasan adadin nawa take dasu ba domin duk sanda Haj. Kulu tasa Yisra ta rok'I wani abu awajensa to itama sai yabata kamar yadda yabawa Yusran.

Iyatensuma hankalinsu yabkwanta sosai babu wani damuea ataredasu tunda sunga abin na Abdulmajid yayi mugun sauk'I amma duk da haka Abbi da Amma basuyo sakacin addu 'a ba saboda masu iya magana sunce mugu baida kama watak'ila kwanta bau'na sukayi musu.

Haka dai sukaci gabada rayuwa basu da wata matsala har cikin Yusra ya shiga wata na uku alokacinne kuma al'amarin ya dawo wannan memakon Fatima kan Yusra suka dawo suke matuk'ar firgitata.

Abin yafara ne wata rana Fatima na kicin tana musu d'an wake kamar yadda Yusran ta buk'ata ita kuma tana kallin wani shirin film a arewa kawai, aka nuno wata k'atuwar 'yar tsana kaman jariri atsaye kyam tanata rawa idanunta na zubar da wani irin abu mai kaurin gaske sosai Yusra ta tsorsta ganintama kamar hannu take mik'o mata sai kawai ta mik'e ta isa gaban tv ta kai hannu da niyyar shafa allom tvn kawai aka cafki wuyanta da mugun k'arfi take tasaki wani irin razanannen ihu wanda yai sanadin fitowar Fatima da gudu dagavkicin

Taku maman islam
[10/7, 5:03 PM] Maman Islam: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp

*___________________________________*

💦💧ZATO NE💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI
WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM

Page 16

.....................sosai gaban haj. Kulu yayi wata irin muguwar fad'uwa ta k'urawa 'yar tata ido ko k'ibtawa takasayi.

Yayin da Yusran tacigaba dayi mata kallon tuhuma tanaci gaba da tsananta kukanta.

Sosai haj. Kulu 5aji zuciyarta yana bugawa da k'arfin gaske, tunaninta yadda zata dubi y'ar tata tafad'a mata sana'ar mahaifinta ai wannan ba k'aramin abin kunya bane agaresu 'yarsu tasan da yadda suka raineta suka girmar daita.

Ana cikin haka Alh. Sambo ya shigo kamar anjefoshi fakam fakam, turus yayi lokacin dayaga Yusra zaune tana gurzar uban kuka take yaji zuciyarsa ya tsunke.

Me kuma yasameta take kuka haka kodai itama taga abinda yaganine kardai da gaske wannan shed'aniyar aljanar so take tarabasa da gudan jininsa kwal aduniya.

"Ina bazai yiyuba wallahi"
Yafad'a da mugun k'arfi hankalinsa a mugun tashe, gaba d'aya suka juyo suka kafeshi da ido

wanda maganarsa nema yasa sukasan da zuwansa.

Cikin sauri Yusra ta taso ta rik'eshi tace"dan Allah Abba ka dubeni kadubi rayuwata ka fad'amin abinda yafaru tsakaninka da wannan halittar datakemin barazana da rayuwata?"

Kallonta yake batareda ya fahimci abinda take cewaba, domin shi yanzu aduniya tunaninsa yana kan abinda yakeson k'ullawa wannan banzar shed'aniyar da kuma d'an korenta duna dolene yayi gagarumin shiri akansu.

"Wallahi Alh. Munzali bakaga komaiba indai kace wannan halin zakacigaba dayi kana tunanin bansan duk abinda kakeyiba ne?
Duk tashin da kake cikin dare da ziyaran wajen tsafinka dakakeyi da kuma yaran mutane dakake sawa ana satomaka kana amfani dasu wajen neman duniyarka duk akan idona kakeyinsu kuma da sannu dubunka zata cika Allah baya zalunci kuma baya barin masu zalunci"

A mutuk'ar razane alh. Munzali yake duban haj. Munira kafin yace to wallahi tunda kika sake kika tonomin sirrina taki ta k'are Munira saidai wata bakeba dan haka yanzun zanje na fad'awa iyayenki cewa kin mutu a sakamakon ciwon cikin dana ce kina dashi wanda ni na k'irk'ireshi saboda biyan buk'atar kaina sannan kuma abinda baki saniba Munira nine nayi amfani da matata uwar yarana wajen neman duniyata kuma dukan yarana mata duk nina sulwantar dasu ta hanyar tsafi kuma suna bani duk abinda nakeso,

Sannan asalin wanda na fara sadaukarwa sune iyayena da suka haifeni kinga danna sadaukar da matar data sadaukar da rayuwarta akaina ai bakomai bane,

Yara biyu kawai yanzu suka ragemin d'aya na halak wanda na haifa ta hanyar aure d'ayar kuma bata hanyar aure na sametaba kuma da matar aure kuma Allah ya jarabceni da tsantsar k'aunar wannan shegiyar 'yar tawa wanda nakejin dana rasata gwanda na rasa Ammar jinin jikina,

Ina baki wannan amsoshinne na tambayoyin da kika daneni dasu tunda jimawa amatsayin sallamarki da duniya Muniraaaaaaa"

daga haka taji an kwad'a mata wani abu mai k'arfin gaske akanta take ta yanke jiki ta fad'i awajen tana kallo alh. Munzali yafashe da kukab munafurci ya kira iyayenta yace musu tayi mutuwar farat d'aya sakamakon ciwon cikin daya turnuketa daren jiya wannan kenan.

"Abba kaifa nake sauraro ka kafeni da ido da gaskene kai marsafine me shan jinin mutane dama Abba akan haram ka ginani? Abba me yasa kuka kasa bani ilimin addini? amma na boko nayi dgree nayi masters me yasa meyasa tafad'a tareda fashewa da matsanancin kuka.

Sosai hankalin iyayennata yakai k'ololuwa wajen tashi duk duniya idan akwai abinda yake d'aga musu hankali bai wuce damuwar tilon 'yarsu Yusra dan haka aka rasa mai bata ganshashiyar amsa atsakanin iyayennata duk sai kame kame har zuwa lokacin da Abdulmajid da Fatima sukazo daukanta.

Kafin lokacin kuwa tayi wani irin wujiga wujiga da ita tayi fayau ta d'ashe saboda damuwar datake fama da ita.

Ko motama sai faman lallashinta suke domin ta masifar d'aga hankalinta.

Suna zuwa gida tana bud'e d'akin taganta zaune gefen gadon ta d'ora kafarta d'aya akan d'ayar tana lila da k'arfi Yusra tace innalillahi wainna ilaihi raji un, take taji wani abu yana bin jikinta koda ta duba jinine wani irin mummunan fad'uwa taji gabanta yayi musamman da ta tuna halin da Abdul da Fatima zasu shiga akan wannan babban asaran da suka tabka.

D'agon kan da zatayi taganta tana lasan jinin dayakevin k'afarta kafin ta d'ago tace mata "naji shi'awar d'an tayine sai na tuna ashefa inadake gashi kuma yana da dad'i zan d'aga miki k'afa ki k'ara samar min da wani babyn na lashe kafin kema na lamusheki"

Daga haka ta busa mata wata iska mai mugun d'umi wanda yai sanadin sumewarta awajen

Yayin da ihun salatin datayi yayi sanadin haurowan su Fatima saman amugun firgice Fatima tabi jinin dayake malala da kallo yayi take ta fashe da wani irin kuka

Shiko Abdul yana ganin yadda jini yake gudu ajikin Fatima ya tabbatar yayi missing babynsa take idanunsa suka canja kala sukayi wani irin ja

Muje zuwa
Takuce maman islam
[10/7, 5:03 PM] Maman Islam: بسم الله الرحمن الر حيم
*______________________________________*

☀️ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀️

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*________________________________________*

💦💧ZATO NE 💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI
WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM
DAGA MARUBUCIYAR
ABINDA YAKE RAINA
WAYYO RAYUWATA

Page

..................k'amewa tayibabakin k'ofar cikin tsansnin tashin hankalin abinda take gani take ta

murza idonta tasake murzawa 'yar tsanace 'yar tsanafa ta cikin tv.

Take jikinta yafara wata irin tsuma takama addu'o'I tana takawa cikin tsan tsar tsoro da tashin hankali yayin da.

Zuciyarta take tunanin daman ba k'yalesu akayi ba kenan, to me hakan yake nufi kuma dataga an juyo kan Yusra?

To wai me hakan yake nufi yaxama dole tayi "binciken abinda yake binsu.

Ihun Yusra ne yayi yawa ta k'arasa cikin sand'a ta d'an dafata take ta fad'I kasa sumammiya takebFatima ta fashe da wani irin kuka.

Sai da tad'an jima a haka kafin tayi dabaran tashi ta haye sama dan d'aukar wanta takira Abdulmajid.

Wata irin dariya yake b'ab'b'akawa har yana fad'uwa k'asa kafin yace "saini mai burin mulakar duniya na kusa cika miki burukanki ya shugabata, burukanki sunabda wuyar gaske cikin mutum ashirin da tara dakika buk'aci nakawo miki kisha jininsu harda matata da wan matata da kuma yaronta.

Sai kuma yafashe dakuka kafin yace ina son matata, ina matuk'ar sonta tana da kirki tana da hak'uri bata tab'a b'atamin ba amma akan neman duniya na sadaukar da ita.

Sai kuma ya fashe da kuka mai had'e da dariys kafin yace shege kud,I kunsakani abubuwa da yawa akanku na rasa abu dayawa zancigaba da rasawa yana cigaba da b'ab'b'aka dariyan yana birgima ak'asa kawai sai gashi yazama k'aton mage ya d'ane kantaga da gudu

A hankali ta, bud'e idanunta tana bin ruwan dayake shiga cikin jikinta kallo d'an juya idanunta tayi ta saukesu akan Fatima wacce tayi tagumi da duka hannayenta idanunta yayi jajir da alama kuka tayi,.

Yanayin d'akin tabi da kallo ko ba'a fad'a mataba tasan asbiti ne, take kuma abinda yafaru ya rik'a dawo mata kamar amajigi  wani irin kuka tafashe da mai k'arfin gaske wanda yai sanadin da Fatima ta zabura ta mik'e tayo kanta tana fad'in " sannu 'yar uwa kin tashi bari na kira likita" daga haka ta fita da sauri har tanacin karo da Abdulmajid wanda yake k'ok'arin shiga d'akin kedan hannunshi suka watse.

Rik'eta yayi a tsorace yace "ke me yafaru?
Wani abunne yasami Yusaran?
Ta farkane?"

Yajero mata tambayoyin ganin yadda ta fito arud'e, ganin yadda yake jera mata tambayoyi da alama shima baya cikin na tsuwarshi yasa ta d'an shafi fuskarsa tayi murmushin k'arfin hali tace "karka damu, dama ta tashine zan fad'awa likita" ajiyan zuciya ya sauke kafin yace "na godewa Allah koma cikin ni bari na kirashi'

Har lokacin bata daina kukan ba jiki asanyaye ta k'araso kusa da ita tace " haba 'yar uwata dan Allah ki daina kukan hakan ya isa mugidewa Allah dayasa babu abinda yasamu babynmu likita yace wani abune ya firgitaki amma babu abimda yafaru dake ko babynmu kinga sai mugidewa Allahko?.

Hannun ta Yusran takamo ta rik'e gam acikin nata tace "'yar tsanafa 'yar uwata 'yar tsana acikin tv ta zuro hannu tashak'emin wuya kinsan ma abinda tace min?"
Tafad'a tareda zubowar wani hawayen mai yawan gaske.

Girgiza mata kai Fatiman tayi itama nata hawayen na k'ara yawaita tace " a' a

"magana fa tayimin 'yar uwata 'yar tsanafa take cemin itace ajalina wai mahaifina yai silan

mutuwar 'yarta dan haka akaina zata d'auki fansa, abin tamabayar anan dama mahaifina d'an shan jinine ban saniba?
Dama duk wannan daular arzikin kud'in haram ne?
dama akan haram muke ginuwa bansaniba 'Yar uwata?
Da sauri Fatima ta toshe mata baki tana girgiza mata kai alamun tadaina fad'ar hakan,

Janye hannun Fatima tayi yayin da wasu zafafan hawayen suka kuma fito mata tace "barni nayi magana 'yar uwata harka da matsafannan yana da matuk'ar wahala tunda tace saita kasheni inkinga ta barni to ki tabbata kwanana bai kareba" tafad'a dawata irin murya mai ban tausayi sannan tacigaba da fad'in.

Na tabbata mommyna tasan sana 'ar mahaifina domin kuwa ita d'in muguwar 'yar bin bokaye da 'yan tsubuce nasan ko awannan yawin dole wani zai fad'a mata sana'ar mijinta, na shiga uku na Fatima iyayena basu kyautawa rayuwataba da suka kasance masu son kansu tafad'a tareda fashewa da wani irin kuka.

Dai dai lokacin Abdul suka shigo da likita ya k'araso da sauri ya rik'o hannunta cikin damuwa yana kallon yadda take gabzar uban kuka kafin yasamu da k'yar yace.

"Dan Allah kidaina kukannan haka kinga k'anwarkima tana kuka"

Hannun nasa ta rik'e gam gam tace "dan Allah ka kaini gidanmu ina son ganin mommyna"

Kallonta yayi sosai da tausayinta a fuskarshi kwance yace "zan kaiki amma sai kin daina wannan kukan.

Kusan awa guda kenan tunda ya kawota gidan takasa cewa mommynnat komai sai uban kukan

datakeyi.

Ita kanta haj. Kulu bak'aramin tashi hankalinta yayiba ganin yadda tilon 'yartata ta wani fige lokaci guda ga kuka tasata gaba tanayi.

Gyara zamanta tayibkafin ta daure tace "Yusra dan Allah idan bazaki fad'amin damuwarkiba to kitaimakeni kidena wannan kukan jifa yadda zuciyana take bugawa saboda tashin hankalin da nake ciki adalilin wannan kukannaki"

Kallonta tayi tace "mommy menene sana'ar mahaifina?????

Muje zuwa taku

Maman islam
[10/7, 5:03 PM] Maman Islam: بسم الله الرحمن الر حيم
*________________________________________*

☀ *FIRST CLASS WRITER'S ASSOCIATION* ☀

FCWA

*{Home of qualities and trusted writer's of The nation}*

https://www.facebook.com/First-class-writers-Association-111719967001810/?referrer=whatsapp
*__________________________________________*

Ina mutukar mika sakon godiya ga masoyana kwarai naga yadda kuka damucdani abisa jina da kuka yi kwana biyu hakan yasamune sakamakon ziyara da nakaiwa yan uwan garuruwa so

alhamdulillah na dawo lafiya kuma na gode da addu'o'inku ina mugun sonku Love u all my heart

💦💧ZATO NE💧💦
NA
HASSANA ABDUL AZIZ YAKASAI
WRITTEN
BY
MAMAN ISLAM
DAGA MARUBUCIYAR
ABINDA YAKE RAINA
WAYYO RAYUWATA

Page 17

.......................da mugun gudu suka k'arasa inda Yusra take yasha inda jini yake malala daga jikinta ba k'aramin tashi hankalinsu yayiba ganin yadda jinin yake gudu.

Da karfi Abdulmajid ya dagota ganin take wata irin jijjiga idanunta suna k'ak'k'afewa ba Fatima ba hatta shima fashewa yayi da wani mugun kuka mai k'arfin gaske yayinda ya ciccib'ota akafad'arsa yai waje daita da gudu Fatima ta bishi babu mayafi babu takalmi.

Tun bayan da Yusra tabar gidan suka koma suka zauna jigum yayin da hankalinsu yake amutuk'ar tashe da k'yar haj. Kulu ta subi alh. Sambo idanunta na zubda hawaye tace "alh. Kaga irin abinda nake fad'a maka ko?
Shiyasa tunda farko nace maka wannan hanyar abarta kodan tilon 'yarmu amma kak'i yanzun ga abinda muka binne shekaru talatin yana shirin bayyanuwa tafad'a tareda sakin matsanancin kuka tace tarihi yana shirin maimata kansa na shiga ukuna ni Kulu".

Sosai take kuka tana dana sanin abubuwa da dama wayyo rayuwa son zuciya baiyi ba wallahi.

Shi kam Alh. Sambo kasa cewa komai yayi domin kwata kwata baya cikin nutsuwarshi hankalinshi amutuk'ar tashe yake yana sane da zuwan wannan ranar amma bai tab'a tunanin zata zomasa kwana kusa ba.

Tun tana ganin dishi diahi har ganin nata ya d'auke gaba d'aya take alh. Munzali yakira wasu k'artin banza suka janye masa ita suka aje wacce yasa aka sakawa irin fuskar hajiya munira sak awajen tareda dunk'uleta waje guda hannunta saman cikinta alamun tana murk'ususu ta rasu.

Wata irin mahaukaciyar dariya ya kece da ita sannan yasakarwa kansa kirari sannan kuma naga ya had'e rai tareda fashewa da kuka.

Haka iyayen haj. Munira sukayi jana izarta cikin tsananin bakin cikin rashin kamilar d'iyar tasu da sukayi yayin da alh. Munzali yake kuka kamar ransa zai fita.

Suko su Abdulmajid koda suka kawo asbiti abinda yai mutuk'ar gigitasu ya d'aga musu hankali shine ganin yadda gaba d'aya jinin da yab'ata musu jiki da wanda ya yake bin jikin Yusra ya bace b'at, babu ko alamunsu k'asan motarsa yakai dubansa inda ya b'aci da jinin, Abdulmajid yakai dubansa take yaga wajen tas babu alamun wani jini take gabansa yai wani irin mummunan fad'uwa.

Ita ko Fatima dubanta takai kan Yusra dataga kamar tana motsi atake Fatimar ta sandare awajen sakamaon idanun Yusra da Fatima tagani yana wata irin ci da wuta ga kuma wasu irin halittu a ciki suna k'yalk'yala mata dariya, take Fatima ta sume ajikin Abdulmajid tsabar gigita da rud'anin data shiga.

Jin fad'owarta jikinshi yace "Fatima yanzun ba lokacin kuka bane wannan abun addu'a yake buk'ata tashi kiga mu fara kaita a duba mana lafiyarta tunda nayi imani har ga Allah wannan cikin mun rasashi kuma nasan tabbas aikin matsafan nanne wallahi Fatima nagaji da wannan masifar yazama dole nayi fito na fito da wannan azzaluman"

Jin duk maganganun da yake shiru babu amsa yasa hannu yad'agota "innalillahi wainna ilaihi raji un" yafad'a da k'arfin gaske wanda har saida ya yajawo hankalin wasu mutanen tareda ma aikatan wajen da gudu suka kawo masa temakon gaggawa aka kwaahe su akayi emmagency dasu, yayin da Abdulmajid ya kifa kansa saman sitiyarin motar wata irin zazzafan kwalla ya kece masa.

"Kana sane sarai da matsalar da kaja mana ko abisa wannan hukuncin daka yanke akan matarka Munira?
To ka shirya wa kanka abinda zaka kare kanka dashi awajen shugaba"

Take hankalin alh. Munzali yayi mugun tashi idanunsa sukayi wani irin ja yace "to yazanyi Asma'u bani da wani zab'in da yafi wannan domin tariga da tasan komai ammafa ba kasheta nayiba kawai dai anbuga mata sandar tsafi atsakiyar kaine kin sani sarai zata farfad'o nanda shekara guda cikin bacewar hankali.

Suna cikin tattaunawar ta bayyana agansu cikin shigar daya d'agawa kowa hankali domin muddun tayi wannan shigar to babu lafiya,

Take gaban munzali da Asma'u ya yanke ya fad'a suka kalli juna cikin fad'uwar gaba amma basu iya cewa komaiba.

Sanye take cikin bak'ak'en kaya yayin da k'wayar idanunta ma yasance bak'i k'irin idanun suna fitar da wani irin hayak'i.

